WANKA DA GARI...

©FATIMA SUNUSI RABI'U
Ummu Affan

*Fatan alkhairi ga ƙanwata ta gaban goshi Dr Maryamah Ibrahim Sokoto, ina miki fatan alkhairi a ko da yaushe, Ubangiji Allah ya baki miji na gari ya albarkaci rayuwarki.*

_Gargaɗi da babban murya, ban amince a ɗaura mini littafi a ko wacce kafa ba, musamman masu youtube channel kar a fara ba tare da izinina ba, duk mai buƙata ya mini magana a dukkan littafina ina ajiye lamba, don Allah kar a fara domin bazan lamunta ba._

*Book 1 Page 1-2*

_Unguwar Rimi Kaduna State._
_2015_

Zaune ta ke a gefen makeken gadonta hawaye ne wasu ke bin wasu a kan kyakkyawar fuskarta, ta ra sa dalilin me yasa Abban Yusra ke mata wulaƙanci, rabon da ta gan shi yau kimanin wata biyu kenan. Me ya ke nufi da irin wannan wulaƙancin na rashin kwana gida? Wayarta da ke gefen gado ta ɗauko, lambarsa ta danna wa kira, ringing ta ke amma har ta ƙarati ɓurarinta ta gama ba alamun za'a ba ta agajin gaggawa, kira na biyu ma haka tayi sai a na uku ya ɗauka. Tun kafin ta maganantu ya riga ta cewa, "Waike wacce irin mayya ce? Na ce ki daina kirana amma kin ƙi! K so ki ke sai na saɓa miki?"
Cikin sanyin murya ta ce, "Haba Abban Yusra me ya sa ka ke mini haka? Kar fa ka mante da Sakinarka ka ke magana."
"Sakinaa ki kiyaye ni tun kafin ranki ya ɓaci." Ya furta a ƙufule.
"Tun yaushe kuma? ai raina tuni ya ɓaci, ka tausayi mini Habibi."
Dogon tsaki ya ja tare da yanke kiran.
Miƙewa Sakina tayi cike da ɓacin rai, A fili ta furta "Me ke shirin faruwa da ni? Me na maka ka ke son ramawa ta wannan hanyar, wanne irin zunibi ke bibiyar rayuwata har haka?"
Mayafinta da key ta zara tayi waje da sauri, moto ta ɗauka tayi mata key ta fita a sittin har Baba Maigadi na cewa,
"Yau me ke damun uwar ɗakina? Duk inda zaki Allah ya kai ki lafiya."
Kai tsaye gidan Hajiyar Abban Yusra ta nufa, tana zuwa tayi hurn me gadi ya buɗe mata katafaran gate ɗin gidan ta tura hancin motarta. Guri ta samu tayi parking sannan ta fito, ƙofar da zata sada ta da parlourn gidan ta nufa, tana shiga ta iske Hajiyar Hamshaƙe kan ɗaya daga cikin kujerun alfarma da sukawa parloun ƙawanya. Ta ɗaura ƙafa ɗaya kan ɗaya tana wani jujjuya su alamar ji da kai da kasaita irin ta jinin sarakuna.

Sallama tayi Hajiyar ta amsa kamar me ciwon baki.
Har ƙasa ta duƙa ta na ƙoƙarin gaisheta, hankali ta amsa.
Cikin sauri Fatima ta ɗago ta kalleta da ta tuna yadda Hajiyar ke ƙaunarta, idan kuwa tazo gidan tayi ta nan-nan da ita kamar ta goyata don so, ai kuwa dole ta sha mamaki ganin yadda yau Hajiyar ta tarbeta.
"Daman Hajiya wajenki nazo."
"Ai gani kin ganni, ko namujiyarki sun fara makancewa ne?"
Hajiyar ta furta cike da gatse.
Sakina ta ɗaura da cewa, "Kiyi haƙuri daman nazo ne don Allah ki tambayi Abban Yusra ko wani laifin na masa ni na tambayesa yaƙi sanar da ni ga shi sai wulaƙanta ni ya ke."
"Ai daman ke abin wulaƙantawa ce, to mene ne a ciki domin ya wulaƙanta ki? Nifa ban cika son yawan kawo ƙara ba, sannan kin fi kowa sanin farin cikin ɗana shi nake so fiye da komi a duniyar nan."
Sakina ta kalli Hajiyar cike da mamakin jin furucinta, zata iya rantsuwa akan tunda ta ke ba ta taɓa kawo wa Hajiya ƙarar Abban Yusra ba amma ta ce haka.
"Allah ya huci zuciyarki idan na ɓata miki rai." Sakina ta furta cikin sanyin jiki, tabbas da walaki goro a miya, domin dai ta san ruwa ba ya tsami haka banza.
Cike da masifa ƙufula ta ji muryar Hajiyar a massarafar sautinta.
"To idan mafarki ki ke ya kamata ki farka Sakina kuma idan baki sani ba ma yau ki sani, wannan yaron dai aure ya ƙara yau kwana biyar suna ɗayan gidan shi.
Da sauri Sakina ta miƙe, tabbas a rina kafin a kiɗime ta furta,
"Aure! Aure!! kuma?"
"I aure, ni ce na ce karya sanar miki da kaina zan sanar da ke, saboda mugun ɓakin halinki da zafin kishinki. Yanzu dai tunda an ɗaura kin ga ba yadda kika iya da shi, shekara har nawa ku ke tare ai ya miki adalci."
Zaman 'yan bori Sakina ta tsinci kanta da yi kafin ta ƙaƙalo murmushin yaƙe,
"To ni a suwa? Wai ɗan wake da gatsine, ban da abin ku mane ne na ta da hankali ko da an sanar da ni?"
Tsaki Hajiya ta ja 'Mtsuuuww!' Tare da furta, "Idan ma zaki da mu, ke ki ka sani don nasan shegen baƙin kishinki na tsiya da gado."
Miƙewa Sakinaa tayi domin muddin tana ci gaba da sauraran waɗannan muyagun kalaman na Hajiya, to za a iya haihuwar guzuma, uwa a kwance 'ya a kwance.
"Ni zan wuce saboda su Yusra sun kusan dawo
makaranta."
Taɓe baki tayi tare da kau da kai.
"Umma ta gaida assha."
Sakinaa ta fita da sauri ta shiga mota, kai tsaye ɗayan gidan Abban Yusra ta nufa, tana zuwa tayi parking a bakin gate ɗin gidan ta fito tare da ƙwanƙwasa gate ɗin gidan.
Maigadi ya leƙo yana cewa,
"Wane ne?"
Ganin matar Oga ce ya yi saurin zubewa yana kwasar gaisuwa, kasancewar ya santa sosai, a baya suna zuwa gidan kafin su fara samun matsala da shi. Ta amsa tana ƙoƙarin shiga ciki.
Sosa ƙeya ya yi, "Am...am..ma Hajiya kamar ya fita." Ya faɗa muryarsa na ɗan rawa,

kasancewar ya ba shi umarnin kar ya bar kowa ya shiga gidan. Ko kula shi bata tsaya yi ba tayi gaba.

Shigarta ke da wuya ta iske su kwance kan doguwar kujera, sallama ta masu gaba ɗaya suka juyo. Sakinaa ba ƙaramin furgita tayi ba, ganin wacece Amaryar, wacce ke kwance kafaɗar Abban Yusra, hakan ne ya ƙara tabbatar mata ita ce amaryar da ya yi.

Ba kowa ba ce Amaryar fa ce Aminiyarta ƙawarta ta ƙut-da-ƙut Zaliha. Nunata ta rinƙayi da hannu bakinta na rawa, cikin rawar murya ta ke cewa,

"Zal...Zali...ha daman ke ce Amaryar Abban Yusra?"

Zaliha ta tashi cike da taƙama da gadara, "Ni ce sai me? Ko haramun ne aurena da shi domin kina ƙwata?"

Sakinaa ta ce, "Tabbas buri yana kama da mutum, amma Zaliha kin yi kuskure. To bari kiji baki isa ba kuma kin yi ƙarya ki ce za ki yi kishi da ni, ni nafi ƙarfinki wallahi sai kin ga ne kuskuranki."

Wani farr da ido Zaliha tayi kafin ta ce, "Sakinaa ke ce zaki ga ne kuskurenki ba ni ba, domin ke ce ki ka yi kuskure a rayuwa ni nan da kike gani da yar dar iyayena na auri Abban Yusra ke kuwa fa? Kin ga ke kin zaɓi farin cikin zuciyarki a kan faranta ran iyayenki, kin ƙi bin umarninsu daga ƙarshe ki ka guje su, ke kina tunanin za ki ga farin ciki a rayuwarki?"

Wasu zafafan hawaye suka gangaro kan fuskar Sakinaa, ta kalli Abban Yusra.

"Ka na jin irin munanan kalaman da take bina da su ko. Amma kayi shuru?"

Shi ma miƙewa ya yi ya furta.

"To me zan ce? Me ma ya kawo ki gidan nan? Ke wacce irin natacciyar mace ce haba abin naki wallahi ya fara isa ta haba!" Ya ƙarashe da ƙaraji.

Da sauri ta kalle shi na mujiyarta jawul kamar jan gauta.

"Ni ka ke furtawa irin waɗan nan munanan kalaman? Babban Yusra Sakinaa ce fa?" Ta ƙarashe da shassheƙar kuka.

Dariyar ƙeta ya yi, "To abin da yaci doma, ai ba zai bar awai ba. ko kin wuce a furta miki haka ne? Wallahi gab nake da furta mummunar kalma ki a kan ki." Ya kama hannun Zaliha.

"Mu wuce ciki ko na san idan kina kallonta ranki ɓaci zai yi."

Ta langwaɓar da kai "My ni fa nafi son mu koma can gidan da Sakinaa take yafi mini, ga shi da girma kuma."

"Duk yadda ki ka ce haka za a yi tawan, ki bari anjima sai mu wuce ko?"

Sakinaa ko saboda tsabar baƙin ciki da takaici fita tayi a fusace ta shiga motarta tayi gida, Allah ne ya kai ta lafiya amma tuƙi kawai take idanuwanta na rufewa, tana zuwa ta faɗa kan kujera ta saki wani rikitaccen kuka tana faɗin..

"Na tuba Abba da Umma ku taimaka ku yafe mini, nasan haƙƙinku ne ke bibiyata ga shi wanda na zaɓa a kan ku yana wulaƙan ta ni ya guje ni.

Ta ƙara fashewa da kuka, na tsantsar baƙinciki da takaici ga kuma damuwa.

Tana cikin wannan halin sai jin muryar Hajiya tayi da ƙarfi tana cewa,

"Ɗiyar matsiyata wacce ubanta ke yawo kullum cikin rana sai ka ce a kan shi talauci ya ƙare."

Sakinaa tayi saurin miƙewa tsaye, cike da jin zafin kalaman Hajiya ta ce,

"Duk abin da zaku mini daga ke har ɗan ki kar ku kuskura ku sake cin zarafin iyayena, domin ba zan taɓa yadda da hakan ba."

Hajiya ta riƙe ba ki, "To fa, tabbas da sauran rina a kaba. Rashin kunya zaki mini mara mutunci,

ke kin san mutuncin iyayen naki ne zaki ƙi bin umarninsu ki ƙi musu biyayya akan abinda suka zo miki da shi?"
Sakinaa wucewa ta yi domin bazata iya sauraron waɗannan munanan kalaman na Hajiya ba. Ita kuwa Hajiya taci gaba da sababinta, sai zagin Sakinaa take da iyayenta, daga ƙarshe ganin taƙi biye mata sai ta kira wayar Abban Yusra ta saki kuka, "To wannan yaron kazo gidanka yanzu ga Sakinaa nan sai zagina ta ke kamar zata rufe ni da bugu." Sakinaa na daga ɗaki tana jin ta sai dai girgiza kai kawai tayi tana matsar hawaye.
Hajiyar zama tayi a parlour tana jiran ƙarasowarsu, domin Zaliha ce ta kirata cewa Sakinaa taje gidansu, tare da faɗa mata ƙarya da gaskiya, shi ne dalilinta na zuwa gidan. Ko minti ashirin ba ta cika ba sai ga su. Hajiyar sai kukan ƙarya ta ke suka isketa, kai tsaye bedroom ɗin Sakinaa ya nufa, yana zuwa ya fara bugun ƙofar kamar zai ɓallata, da ya ke ta saka key.
Faɗa ya ke, "Ba za ki zo ki buɗe ba sai na ɓallata?"
A hankali ta tashi taje ta cire key ɗin da ta saka. Aikuwa tana cirewa ya turo ƙofar ya rufeta da bugu daman da belt hannunsa, kuka take da ihu amma buguntа yake su Hajiya na gani sai ma zuga shi da take, sai da ya mata ligi-ligi sannan ya barta kwance.
Da ƙyar Sakinaa ta iya jan jikinta ta shiga toilet ta gasa jikinta tana kuka, bayan ta gama ta ɗauro alwala ta fito ta canza kaya, tayi sallar azhar da ake kira sannan ta kwanta nan ta ke barcin wahala ya kwasheta.
Wajen ƙarfe biyu na rana ta fara jiyo hayaniyar su Yusra alamar sun dawo makaranta, ta tashi da sauri. Fahat ne ta ga ya shugo yana kuka.
"Babana me yasa me ka." Ta tambaye shi a rikice.
"Yunwa na ke ji Mami"
Tayi saurin miƙewa domin ta man ta sam bata ɗaura musu abinci ba, ta nufi kitchen domin ɗaura musu girkin, bayan ta gama duk abinda zata yi ta tsayar da ruwa, ta fito taje tayi musu wanka ta canza musu kananun kaya, ta rungume Fahat da har yanzu yake kukan yunwa, domin ba shi da juriyar yunwa, sai rarrashin shi ta ke. Suna haka Abbansu ya shugo ya iske su.
Yusra ta ruga da gudu ya caɓata sama ya rungume yana dariya.
"Oyoyo Abba."
Shima Fahat ya taho yana ƙunƙunai, ya ce"Me ke damun Fahat ɗin Abba?"
"Yunwa na ke ji Abba kuma Mami ba ta gama girki ba."
Miƙewa ya yi tsaye ya kama hannun yaran sannan ya gallata mata wata muguwar harara.
"Ku tashi muje gidan Hajiya muci abinci ko."
Yusra ta ce, "Abba Mami ta shirya muje da ita?" Kasancewar ada tasan idan har zasu fita to dukansu suke fita.
Ya ce, "A'a Mamana kin ga Mami na aiki."
Fahat ya ce, "Amma zamu yo bata take-way ko Abba?"
"I."
Kawai ya amsa musu suka wuce.
Hawaye kawai Sakinaa taji suna kwarara a fuskarta, lallai ɗan adam butulu ne domin yau ga shi Abban Yusra ya yi mata butulci haka ƙawarta mafi kusanci da ita Zaliha, me yasa taƙi bin umarnin iyayenta? Sai yau ta tabbatar lallai tayi gudun gara ne, ta faɗawa gidan zago.
Tashi tayi ta nufi kitchen domin duba abinda ta ɗaura, me zata iske? Zaliha ta gani ta sauke mata girki tana yin nata a wajen bayan kuma gas ɗin ba ɗaya ba ne.

"Zaliha me yasa baki neman zaman lafiya?" Zaliha tayi shewa tare da buga cinya ta ce"Lallai Sakinaa ke zaman lafiya ki ke so ayi a gidan nan? Ai ba ke ba zaman lafiya a gidan nan, nayi alƙawarin sai na ƙuntata rayuwarki."
"Ke ba ki isa ki ƙuntata mini ba kuma ina son ki sani, ai wanka da gari ba shi maganin yunwa sai an sha kuma na san duk wani hali da zan shiga daga Allah ne.."
Tana kammala faɗar hakan.......
08104335144

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUku
#LabarinSakina_Gawurtattu uku 2024_

WANKA DA GARI...

FATIMA SUNUSI RABIU
Ummu Affan

*Book 1 Page 3-4*

Tana kammala faɗar hakan tayi wucewarta, daman saboda yaranta za tayi girkin kuma sun fita da Abbansu faƙat.
Zaliha kuwa taji haushin kalaman Sakinaa don haka ta ɗau alƙawarin sai ta yi wa Sakinaa sharrin da sai tayi da na sanin abinda ta faɗa mata.
Ko da su Abban Yusra suka dawo Sakinaa ko leƙowa ba tayi ba, yaranta suna shugowa tayi sauri ta musu shirin islamiyya ganin lokaci ya kusan ƙurewa sannan ta rakasu har gurin Direban da ke kai su makaranta.
Tana dawowa daga rakasu ta iske Abban Yusra da Zaliha a farlour, za ta wuce bedroom taji yana kiranta. Tsayawa tayi ba tare da ta juyo ba, bai damu da yadda tayin ba ya ce,
"Tun da kin hana Zaliha ta dun ga shigar miki kitchen sai ka ce ke ki ka gina sa? To daga yau ke zaki din ga mata girki duk abinda take so za ki dafa.
Da sauri ta juyo ta kalli Zaliha cike da mamakin jin irin sharrin da ta mata.
"Haba Abban Yusra yan zun ni ce zan zama mai girkin Zaliha sai ka ce wata 'yar aiki, ai ba abin da ka ɗauke ni kenan ba."
"To da me ki ka dace? Ai wallahi yafi kyau ma a ki raki da 'yar aikin don matsayinku guda ne yanzu a wajena." Ya faɗa yana wani hura hanci.
"Shi ke nan." Tana faɗa ta wuce ba tare da ta kuma cewa komai ba.
Tun daga ranar Sakinaa ba tayi ƙasa a gwiwa ba ta zamo ita ke yin komai na gidan duk Zaliha

tasa ya kori 'yan aikin gidan Baba Maigadi kawai aka bari sai Direbansu Yusra, hatta wanki da guga ita ce. Daman tana wanki idan ta so, haka ba ko wanne kaya take bayarwa ba, guga kam tana ci mata rai.
Yaranta Yusra da Fahat Zaliha ta ɗau ɗawainiyarsu sosai take kula da yaran, shirinsu zuwa School da islamiyya haka fannin abincinsu ba ta wasa, ko a da can Zaliha me ƙaunar yaran ce.
Hajiya kuwa kusan kullum sai tazo gidan tayi tawa Fatima tujara da habaice-habaice, tayi ta tsine mata ita da iyayenta, wani sa'in ma su ukun suke haɗuwa suyi ta mata rashin mutumci da tujara, maƙaƙen maganganu kuwa tana shan su da gori.
Fatima ba ta da kwanciyar hankali wuni kuka, tayi duhi ta jeme tayi baƙi sosai ta rame kullum cikin kuka take saboda tsabar wahala da baƙin ciki.
Wata rana tana zaune a kitchen tana aiki ta jiyo muryar Hajiya na kiranta, tashi tayi da sauri har tana tuntuɓe ta zube a gabanta.
"Hajiya ashe kin zo barka da zuwa."
Hajiya ta daka mata tsawa, "Ya isa haka, yau dai zamanki yazo ƙarshe a gidan nan." Sakinaa ta kalli Hajiyar da sauri ta ce, "Me nayi kuma Hajiya? Ki rufa mini asiri na mutu maza su kai ni, don Allah kar ki tozarta ni, idan ba ki kalle ni ki duba su Fahat."
Zaliha ta taɓe baki, "Ƙwarƙwasa raka kishiya biki, yau dai ƙarya ta ƙare sai a koma gida aci gaba da cin tuwon dawa miyar kuka daman da shi aka raine ki."
Hajiya ta ce, "Hakkun kuwa sai a gaida me dattin hula, da mai baƙin ɗanƙwali." Zaliha ta saka dariyar mugunta tare da buga cinya, "A koma can idan ma ya amsheki idan kuma ya ce abi duniya ne to ai gaki gata maraba take da waɗanda ma suka fiki, ke duniya wanda bai zo ba ma jiransa take."
Tuni ruwan hawaye suka tsinke a fuskar Sakinaa Hajiya ta ce, "Wannan yaron inaso ka sallame ta, idan kuma zaka ci gaba da zama da ita to, ni dai naga rabuwarku tafi."
"Hajiya duk abin da ki ke so haka za a yi." Numfasawa tayi "A'a kar ka ce na shiga haƙƙinka."
Takarda da biro ya ɗauko ya yi rubutu ya cillawa Sakinaa yana faɗin, "Ko ɗaya Hajiya ai na yadda ƙwallon mangwaro ne na huta da ƙuda." Ɗauka Sakunaa tayi ta buɗe a hankali saki ɗaya ta gani.
Hawaye ne suka wanke fuskarta kallonsu tayi, sai kuma ta miƙe tsaye ta wuce.
Beedroom ɗinta ta shiga, ta faɗa toilet wanka tayi sannan ta fito, ta shirya cikin wasu riga da siket na atamfa sannan ta sauke ƙaton akwatinta ta zuba kayanta da duk wani abu mai muhimmanci nata, ta zuba takardun makarantarta a ƙaramar jakarta da kuɗaɗenta waɗanda Abban Yusra ke bata kafin su fara samun wannan matsalar, ta sagala jakarta ta jawo a kwatinta ta fito.
Har zuwa lokacin suna Parlour, suka kalleta ta kallesu gyara tsayuwa tayi ta kalli Hajiya da Zaliha ta ce,
"Na gode da abinda ku kai mini ba zan ce komai ba domin nasan ni najawa kaina." Kallon Abban Yusra tayi.
"Kai kuma tsakanin ni da kai wanda ya cutar da wani Allah ya saka ma shi."
Sannan taja akwatinta tana kuka tabar gidan, bata tsaya tambayar yaranta ba domin tasan yadda Hajiya ke ƙaunarsu ba zata ba ta su ba.
Tana fita ta samu a daidaita sahu ta tsayar tahau bayan ta sanar da shi inda zai kaita, suna zuwa ta biya shi kuɗinsa sannan taja akwatinta zuwa cikin gidansu wanda ginin ƙasa ne ɗan

madaidaici, irin na malam Shehu.
Da sallama ta shiga cikin gidan jiki a sanyaye, daga can cikin ƙuryar ɗaki taji ana amsa mata sallama, wata mata ta fito wacce ba Ummanta ba ce, ta gaishe da matar tare da tambayarta, "Umma ba ta nan ne?" Matar ta ce,
"Wacece Umma kuma?"
Sakinaa ji tayi kamar an buga mata guduma a ka, ta ƙarewa gidan kallo tabbas nan ne gidan iyayenta gidan da tayi ƙuruciyarta a ciki ta dawo da kallonta ga matar.
"Ba nan ba ne gidan Malam Abdullahi Bakanike ba?"
"Gaskiya ba nan ba ne sai dai ban sani ba ko waɗanda suka tashi ne ki ke nufi, kuma shekararmu uku a gidan nan mijina saya."
HAwaye ne ke bin fuskar Sakinaa ta ce, "Don Allah ko kin san inda suka koma?" Matar ta ce "Wallahi ban sani ba." Cikin shassheƙa Sakinaa tayi wa matar godiya tare da fita jikinta na ƙyarma, mummanan tsoro ya shigeta ga tsananin tashin hankaki.
Jan akwatinta tayi gaba tana tafe tana kuka, kai tsaye garejin da Abbanta ke aiki ta nufa bayan sun gaggaisa da mutanan da ke wajen waɗanda ba ta san su ba take tambayar ɗaya daga ciki. "Don Allah Malam Abdullahi nake nema." Wani mutumi ya ce, "Wane ne kuma haka?" Tayi masu kwatancen kamaninsa yadda zasu gane, wani dattaju ya ce, "Ai ya daɗe da barin garejin nan kusan shekaru uku kenan."
Nan take tashin hankalinta ya nunku har ya gaza ɓoyuwa a fuskarta. Ta fito garejin tana kuka sosai bayan sun tabbatar mata ba su san inda ya koma ba.
Can nesa da garejin ta samu guri ta zauna bis a wani ɗan dandamali tana kuka, ina iyayenta suka je? Meke faruwa da su a halin yanzu? ta sake sakin wani rikitaccen kuka nan take rayuwarta ta baya ta fara dawo mata, tagumi tayi tana hawaye ta fara tariyo rayuwarta ta baya.

TUSHEN LABARIN

Malam Abdullahi talaka ne sosai sana'arsa Kanukanci wato gyaran moto babura har da kekuna. Malam Abdullahi mutum ne me wadatar zuci duk da shi talaka ne bai hana ya wadata gidansa da abinci da sutura ba domin gidansa ba anemi komai an rasa ba daidai gwargwado yana da ƙoƙarin neman na kansa.
Matarsa ɗaya Hadiza, asalinsu 'yan Bakori ne ƙaramar hukumar jahar Katsina, domin daga shi har Hadizan 'yan can ne, ya je garin Kaduna ne domin neman kuɗi shida abokinsa Saminu, abu kamar wasa har ya dawo da Hadiza nan, tun suna gidan haya har Allah ya buɗa masa ya fara gini don mutum ne me ƙoƙarin neman na kai.
Bayan ya kammala suka dawo garin gidansa, ɗakuna biyu ne a madaidaicin gidan ɗaya ciki da falo sai ɗaya guda sai kuma kitchen da bayi na wanka dana bahaya a waje, ginin ƙasa ne amma ya yi masa fulistar na suminti haka tsakar gidan shafe yake da suminti tas.
Sun daɗe ba su sami haihuwa ba, sai da suka shekara takwas da aure, aikuwa da Hadiza ta samu ciki sun yi murna da farin ciki mara musaltuwa, nan aka dun ga renon ciki da tattalinsa har ya isa haihuwa, ta haifi kyakkyawar ɗiyarta mace.
Sosai suka yi murna da farin ciki da samun ƙaruwar nan, inda ranar suna yarinya ta amsa NANA Sakinaa. Yarinya kyakkyawa wanka tarwaɗa, anyi bidiri don 'yan Bakori sun zo a ka sha bikin suna daga baya suka koma gida.

Sakinaa ta taso cikin so da ƙaunar iyayenta suna ji da ita sosai musamman Abbanta. Abba akwai sanyi ko laifi tayi baya bugunta sai dai nasiha, garama Umma tasha bugunta idan tayi ba daidai ba
Ummanta mace ce mai natsuwa da kamala ga son addini da son mutane, haka Abbanta kowa a unguwarsu yana yabonsa ya samu shaida ta mutane kam.
Shekarar Sakinaa uku Abbanta ya sata boko da islamiyya don yarinya ce mai kazar-kazar ga surutu, ai kuwa ana sata baki ya ƙara buɗewa gata da ƙoƙari sosai.
Abbanta ke kaita boko da safe biyu na rana ya ɗaukota, idan yaci abinci ya koma wajen aiki daman da ya kai ta da safe yake wucewa aikin, idan yaci abinci ya koma huɗu na yamma yazo ya kai ta islamiyya, ƙarfe shidda ya ɗaukota su dawo gida shi ma daga lokacin ya dawo aiki kenan sai ya yi wanka ya fita masallaci sai anyi isha'i ya ke dawo wa daga nan kuma su zauna baranda su ci abincin dare sai ya yi wa Sakinaa tatsuniya da haka har tayi bacci sannan su je su kwanta. Haka rayuwarsu ta ke har zuwa lokacin da ta iya zuwa makaranta da kan ta.
Lokacin shekarunta goma, har abinci ita ke kai wa Abbanta gareji.
Ƙawarta wacce suka shaƙu sosai da ita itace Zaliha ɗiyar baƙotansu ce, kaf unguwarsu da ita aka san ta, kullum tare suke zuwa makaranta boko da islamiyya ajinsu guda ne.
Shekarun Fatima sha biyu ne lokacin tana Jss one, ɗin ƙaramar Secondary ta dawo kai wa Abbanta Abinci ne a gareji, tafiya take a hankali cikin natsuwa kamar wata babbar mace.
Shi kuwa yana cikin moto yana kallonta yanayinta ya burge shi, yasha haɗuwa da manyan mata 'yan ƙasar nan da wajenta amma bai ga yarinyar da ta burgesa ba irin wannan ƙaramar yarinyar.
Bin ta yake a hankali cikin mota, ganin ta shiga wani lungu da mota bazata iya shiga ba, sai ya fito ya din ga bin ta a baya, ganin za ta ɓace masa ya sa ya yi saurin ƙara takun sawunsa yana kiran "Ƙanwata! Ƙanwata!!"
Ji tayi kamar daga sama ana kiran ƙanwata sai ba ta wai ga ba, domin a tunaninta ba ita ake kira ba ganin bata da yaya ita ɗaya iyayenta suka haifa.
Jin ana ƙara kusanto ta ana kiran, "Ƙanwata ji mana ko baki son sabon Yaya?" Hakan ne yasa ta tsaya chak tare da juyowa.
Wani kyakkyawan saurayi dogo taga ni yana zu ba mata murmushi, sanye yake cikin ƙananun kaya Jeanse da t-shirt ya yi kyau sosai sumar kan nan nasa baƙ wuluk sai shinning take, hannusa ɗauke da wani agwogwo daga gani zaka gane na gold ne saboda ƙyallin da yake, kana ganin takalmin ƙafarsa zaka ga ne na manya ne domin daga yanayinsa ka san komi na shi na musamman ne.
Ƙaraso wa Ya yi hannayensa zube cikin aljihu ya ce, "Ni suna na UMAR FARUUƘ."
A zuciyarta ta furta.
'Kuji mutum kamar na tambaye shi sunansa,  amma fa sunan ga daɗi kuma suna manya ne, hakan ma na musamman ne.'
"Ke mene ne sunanki?" Ya katse mata tunani da tambaya.
"Ni?" Ta tambaya tana nuna kanta, cike da ƙuruciya. Abin ya ba shi dariya ya ce, "Yes ke ni ba kiji na faɗ miki nawa sunan ba?"
"Sakinaa!" Ta faɗa kai tsaye domin ita ba ta iya ƙarya ba.
"Wow nice name, suna me daɗi kuma babban suna." Murmushi kawai tayi.
"Ni zan wuce kar Ummana ta ji ni shuru." Bin bakinta ya yi da kallo yadda take magana cikin

natsuwa. Murmushi ya yi. "Ummanki ko dai Ummanmu? don haka wuce muje gidan tare."
Cike da mamaki take dubansa za tayi magana ya rigata, "Ko baki son inje incewa Umma tayi sabon ɗa kuma yayan Princess?" Kallonsa tayi "Wace ce kuma Princess?" Cike da yarinta tayi tambayar.
"Ke ce mana, sunanki yana da girma a wajena."
Rufe fuska tayi cike da kunya, murmushi ya yi "Mu je ko?"
A can gida kuwa Umma taji Sakinaa shuru, saɓa hijab tayi zata fito kenan sukaci karo da Abba ya ce, "Lafiya ina zuwa kuma Hadiza?"
"Garejin daman za ni naji Sakinaa shuru."
"Shuru kumakina nufin bata dawo ba? Ai tuntuni ta tafo gida." Dukansu sai hankalinsu ya tashi za su fita nemanta kenan sai ga su.
Kallon-kallo suka fara Umar ya ce, "Sannunku da gida." Ya duƙa har ƙasa ya gaishesu, suka amsa cike da mamaki. Abba ya ce, "Lafiya dai ko yaro? Sam ban waye ka ba?"
Murmushi ya yi "Lafiya ƙalau kawai mun haɗu a hanya ne." Nan Sakinaa take sanar musu abin da ya faru.
Abba ya ce, "A'a shugo daga ciki a shumfiɗa maka tafarma." Ya miƙe yabi bayansu, Umma ta shimfiɗa musu tafarma a barandar gidan.
Umar ya ƙara gaishe da su Abba, suka amsa masa cikin sakin fuska. Ya ɗaura da cewa. "Suna na Umar Alƙasim Inuwa mun haɗu da Sakinaa a hanya shi ne na tsayar da ita muka gaisa har na biyota gida in gaisheku."
Abba ya ce, "Babu komai Ummaru da fatan dai lafiya, ba wani abin tayi maka ba? domin ba a shaidar ɗan yau haihuwarsu ake ba a haifi halinsu ba."
"Babu komai Abba kawai dai haka nake jinta kamar Ƙanwata." Gaba ɗaya sukayi dariya. Abba ya sake cewa, "Ai haka Allah ke ikonSa baka san mutum ba sai kaji ya kwanta maka, kamar yarda nima kallo ɗaya na maka naji kashi ga raina daga ganinka gidan mutunci ka fito."
Umar ya yi murmushi "Na gode Abba ƙwarai nima jinku nake kamar iyayena."
Umar ya daɗe gidan sai da yaci tuwan daren Umma sannan ya bar gidan, yadda suke sai ka ɗauka daman sun daɗe da sanin juna. Wanda wannan ne kuma silar faruwar ko wacce zanen ƙaddara daga rayuwar Sakinaa..
**** **** ****
Da sallama ya shiga katafaran Parlourn gidan. Daddy ne ya miƙ da sauri ya ruƙo shi.
"Faruuƙ daga ina ka ke? Har ka iya kai wa irin wannan lokacin?"
Mummy ta ce, "Ka ta da mana hankali ko abinci mun kasaci Faruuƙ ina ka je?"
Murmushi ya yi.
"Dad an Mum me kuka mayar da ni ne?"
Da sauri Daddy furta "Ƙaramin yaro."
Mummy ta ce, "Jaririma zaka ce Daddyn Faruuƙ."
Ɓata fuska ya yi cike da shagwaɓa ya ce "Duk girman nan nawa amma kuke cewa haka ko aure fa aka mini lafiya ƙalau zamu zauna da matata "
Mummy ta fara tafa hannu ya yin da Daddy ya riƙe baki.
"Faruuƙ aure! Karatun kuma fa?" Murmushi ya yi "To ai naji kuna ce mini ƙaramin yaro ne.
Dundu Mummy ta kai masa ta ce, "Kaci gidanku daga ina ka ke, sai fa ka faɗa mini ko dai taɗin kaje don mu ga ne ka isa auren?"

Zama ya yi kusa da ita ya ce, "Daga gidansu Sakinaa nake." Nan ya sanar musu komai ya ɗaura da cewa "Wallahi suna da ƙyirki sosai."
Mummy ta ce, "Faruuk ba dai saurin yarda ba, kar fa ka ɗauko mana abin da wataran zai saka mu kuka."
"Haba Mummy don Allah ki yi mana fata na gari." Shafa kan sa tayi "Is ok my son tunda kana son su muma dole mu so su." Daddy ya ce, "Wannan haka yake."
Washe gari ya dauki iyayensa sai gidansu Sakinaa, ƙwarai sun yi mamakin ganin gidan, ba su taɓa tunanin talakawa ba ne, haka suka shiga sun ga karramawa gurin Abba da Umma, haka ma Sakinaa
Kallo ɗaya Mummy tayi wa Sakinaa taji yarinyar ta shiga ranta shima Daddy haka.
Tun daga wannan rana zuminci mai ƙarfi ya kullu tsakanin iyalan gidan su Sakinaa da Umar kai ka ɗauka daman 'yan uwa ne su tun usul....
08104335144

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattUku
#LabarinSakinaa
_Gawurtattu uku 2024_

WANKA DA GARI...

_Ummu Affan_

*Book 1 Page 5-6*

Zuwa yanzu su Sakinaa sun kammala ƙaramar Secondary ɗin su, wato JSCE har sun shiga SS1. Ba laifi sun yi girma sun zama 'yan mata amma ba can ba, ba laifi Sakinaa kyakkyawa ce wankan tarwaɗa. Tana da ɗan jiki kaɗan, doguwa amma ba tsowo sosai ba sai dai Allah ya hore mata mazaunai sosai. Sannan tana da cikar ƙirji ga ƙoƙari a makaranta Allah ya ba ta ƙyanwa mai saurin ɗaukar karatu, domin ita ke amsar na farko a ajinsu, iyayenta suna alfahari da ita domin saboda natsuwarta da kamun kai da biyayyarta zuwa lokacin shaƙuwa mai gauraye da wani babban al'amarin da ƙarancin shekarunta ya hanata ganowa shi ke wakana tsakaninta da Hammanta Faruuƙ, shi tabbas yasan yana ƙaunar Sakinaa sai dai ita kawai ta ɗauka shaƙuwa ce a tsakaninsu.
Suna hanyarsu ta dawo daga makaranta, tafiya suke irin ta 'yan makarantar da aka ta so su ƙarfe biyun rana, ga yunwa sannan ga galabaita yadda rana ke dukansu.
Zaliha ta dubi Sakinaa ta ce, "Wai Sakinaa in tambaye ki mana, ya ku ke da Hamma Umar ne?"

Sakinaa ta taɓe baki.
"Yadda na sanar miki ko baki yarda ba ne?"
"A'a kawai na gan shi kyakkyawa kuma ɗan gayu a mota fa yake zuwa duk idan zai zo gidanku."
"Ke dai baki gani ki kyale komai sai kinyi magana, kina ɗaya daga cikin sa'idinawa ana ruwa kuna irgawa."
Dariya Zaliha tayi, "Na fiki ne? Na zata duk ɗaya muke tunda sai hali yazo guda ake ƙawance."
Sakinaa tayi murmushi.
"Uhmm ke dai Zaliha ba dai iya zance ba, ni nan wallahi na ƙosa mu kai gida duk na gaji yasin."
Zaliha ta ce, "Ke dai bari kawai ga shi ana rana yau sosai."
Haka suke tafe har suka kai gidajensu suka wa juna sallama.
Sakinaa na shiga ta iske Hamma Umar yazo, daman tun a waje ta ga motarsa, da murna ta ƙarasa da sallama. "Oyoyo Hamma Umar." "Oyoyo Princess kin dawo?"
"Na dawo Hammana."
Gabaɗaya su ka yi murmushi.
Ɗakinta ta wuce ta cire Uniform taja ruwa ta watsa sannan tayi alwala, bayan ta idar da sallah ta fito cikin wata doguwar riga ta shadda. Umma da Hamma Umar suna zaune suna hira ta ƙaraso.
"Umma sannu da gida." Ta amsa da, "Yawwa." kitchen ta wuce don ɗauko abincinta, me zata ga ni Fate ne, ɓata rai tayi don duk a cikin abinci fate ne ba ta so
Dawowa tayi tana ƙunƙunai da cin magani. Umma ta kalle ta. "Lafiya me ya faru?" Turo baki tayi gaba. "Umma fate ne fa kika yi."
"I na sani ai, ni nayi ko?" Nan ta fara hawaye. "Amma Umma kina sa ne ban shan fate ko?"
Umma ta ce, "Hmmm shagaɓa wai tarwaɗa da kukan ƙishin ruwa, ni dai yau shi nake marmarin sha haka ma Abbanki ga Hammaki ma nan yanzu ya gama sha yana santi." Da sauri ta ce, "Faten?"
"Ƙwarai kuwa, shi Faten ba abinci ba ne?"
"Ni dai Umma ki ba ni abinda zan ci yunwa nake ji."
"Sai kuma kiyi ai, don ni ba ni da komai sai ki jira na dare."
Zubewa Sakinaa tayi tana riƙe ciki tana cewa, "Wayyo cikina yunwa nake ji Umma za ta kashe ni, ta hana ni abinci . Abbana wayyo Abbana kazo."
Mai Hamma Faruuƙ zai yi ba dariya ba, har da tafa hannu Umma miƙewa tayi,
"Sai kiyi ta yi, fate ne idan ba za kisha ba sai kiyi ta zama da yunwarki." Nan fa taci gaba da kururuwa tana burgima.
Hamma Faruuƙ ya ce cikin dariya.
"Wai Princess mene ne hakan? Da girmanki ki ke haka?" Kallon shi tayi cikin hawaye ta ce, "Hamma Faruuƙ Umma fa na sa ne ba na sha shi ne tayi."
"To yanzun ya ki ke so ayi?"
"Kawai ni dai yunwa nake ji, kuma bazan iya kai wa har sai na dare ba."
Miƙewa tayi bari inje gurin Abbana na san zai saya mini abu naci.
Shi ma miƙewa ya yi
"A'a kar ki wahalar da Abba muje na saya miki." Da sauri ta ruga ɗaki cikin murna ta ɗauko hijab taje ta yi wa Umma sallama.

"Allah ya so ki yau Alhamis babu islamiyya da ba inda zaki je." Fita tayi kawai tana murna.
Buɗ mata motar ya yi ta shiga wani ƙamshin daɗi ya bugi hancinta sai da ta lumshe ido, shiga ya yi ya mata key suka tafi, ƙira'ar malam Ahmad Sulaiman na tashi lumshe ido tayi cikin wani sabon yanayi turaren Hamma Faruuƙ na mata daɗi sosai wanda B for B gidan ƙamshi ke haɗa masa. (Turarenta ƙarshe ne domin wallahi ni Ummu Affan na gyada yana kama jiki sosai shi ne turaren da Hamma Faruuƙ ke sakawa, mai buƙatarsa ya tambaye ni zan haɗa shi da B&B gidan ƙamshi.)
Kai tsaye gidansu ya wuce da ita, daman tun a hanya ya kira Mum ya sanar mata suna hanya, 'yar ƙauye Sakinaa ta zama lokacin da suka shiga katafaran gidan su Hamma Faruuƙ, kalle-kalle kawai take, ai hankalinta bai tashi ba sai da suka shiga Parloun gidan, gabanta ya din ga bugawa a ranta ta aiyana ko dai Hamma Faruuƙ sayar da ita yake son yi? Nan fa idanuwanta su kai rau-rau ta kalle shi.
"Hamma Faruuƙ don Allah kayi haƙuri kar ka sayar da ni ka ga ni ɗaya su Umma suka haifa kayi mini rai don Allah."
Dariya ma taba shi kallonta ya yi.
"Ko da ina sayar da mutane Sakinaa bazan taɓa iya sayar da ke ba, ki sa a ranki komi wuya Umar ba zai taɓa cutar da Sakinaa ba." Ajiyar zuciya tayi tana kallonsa, murmushi ya mata ita ma ta mayar masa.
Sama ya wuce, sai gashi suna sakkowa da Mum, nan hankalin Sakinaa ya sake kwanciya ta duƙa har ƙasa tana gaishe ta da sauri Mum ta ɗagota ta rungumeta.
"Kul Sakinaa ta so kin ji 'yata."
Cike da kunya Sakinaa ta gaisheta.
Mum ta ce, "Ya su Ummanki da Abbanki?"
"Suna lafiya ƙalau." Nan ta kira mai aikinta aka cikawa Sakinaa gabanta da abinci da nasha kala-kala, ƙasa tayi da kai cike da kunya, Mum ta ce, "Ki saki jikinki Sakinaa nan gidanku ne ki ɗauke ni tamkar Ummanki."
Ita dai Sakinaa ta kasa cewa komai don sosai take kunyar Mum, ganin haka Mum da kanta ta zubawa Sakinaa komai ta ce taci, miƙewa tayi zata wuce don Sakinaa ta samu taci wani abu Hamma Faruuƙ ya ce, "Kai Mum ni shi ke nan an man ce da ni, ko tayi ba ki yi mini ba?" Da sauri ta zauna kusa da shi. "Sorry my Son me ka ke so?" Ya ce "Abinda ki ka ba ta." Yana nuna Sakinaa da baki, nan ta haɗa masa tana ba shi a baki, ai sakin baki Sakinaa tayi tana kallonsu, a ranta take ai yana daman haka Hamma Faruuƙ ya ke.  Ganin kallon da take musu yasa ya ɗaga mata gira tare da kanne mata ido ɗaya, sannan ya nuna mata gabanta, alamar tayi abinda ke gabanta, murmushi tayi ta fara cin abincin a hankali.
Ba wani sosai taci ba domin daman ba iya cin abinci da yawa tayi ba, turo ƙofar da a ka yi yasa hankalinsu ya koma can, wata budurwa ce ta shugo kyakkyawa zatayi 25 sanye take cikin riga da wando matsatstsu sun kamata sosai sai wani ƙaramin mayafi da ta ɗaura a kanta babu kallabi a kanta hakan yasa kyakkyawan gashin kanta ya bayyana, siririya ce irin sosai ɗin nan, baka iya ganin idanuwanta sakamakon ƙaton baƙin gilashin da ya kusan rufe rabin fuskarta, ta kalmin ƙafarta dogo ne sosai, hannunta mai ɗaure da ɗan siririn agwogwo da shi ta ke jan akwatinta.
Mum ta miƙe da sauri tare da kiran sunanta, "Zubaidaa!" Murmushi tayi tare da nufar Hamma Faruuƙ ta rungume shi, tureta ya yi daga jikinsa yana cewa "Haba ZubaidaA meme ne hakan?"

Murmushi tayi ta ce, "Hamma Umar har yanzun ka na nan da halinka?" Taɓe baki ya yi, "To mai za a fasa mutuwar ko hisabin." Juyawa tayi ta rungumi Mum ta ce, "Nayi missing ɗinki my Mum." Murmushi tayi, "Nima nayi naki 'yata, ya ki ka baro su Hajiya Sakinar?"
"Suna lafiya ƙalau suna gaishe ku sosai."
Umar kallon Sakinaa ya yi wacce ta saki baki tana kallon ikon Allah "Princess tashi in mayar da ke gida kar Umma ta ji mu shuru." Da sauri ta miƙe.
Zubaida ko cikin ruɗu ta juyo cike da kishi jin My Hamma Umar ɗinta ya kira wata da Princess. Kallon Sakinaa tayi nan take taji ta tsaneta kai duk wata mace dake raɓar mata Umar ta tsane ta, tsana mafi muni da munana.
Sakinaa ta katse mata tunani da furta, "Mum zamu wuce na gode sosai." Murmushi Mum tayi, "Mene ne na godiya? Nan fa kema gidanku ne ina zuwa." Sama ta wuce sai gata da wata babbar leda tabawa Sakinaa, girgixa kai tayi "A'a Mum na gode." Ɓata fuska tayi "mene ne hakan Sakinaa? Kema fa 'yata ce kuma babu kyau mayar da hannun kyauta." Hamma Umar ne ya amshi ledar ya ce, "Rabu da ita Mum dole ne ta amsa." Kasa tayi da kai ta duka har ƙasa tana wa Mum godiya.
Ɗagota tayi ta ce, "Lalala babu godiya tsakaninmu, don uwa ta bawa 'yarta abu sai ta ce sai ta gode ki gaishe mini da Ummanki da kyau idan na sami lokaci ina nan zuwa."
"To Mum za taji na gode." Har ƙofa Mum ta raka su sannan ta juyo.
Zubaida da ta kusan sumewa a tsaye nan take ta fara hawaye.
"Mum mece ce wannan? meke shirin faruwa haka? Me ki ke so ki ce mini? Don Allah kar dai ki ce wannan Ƙwailar yarinyar budurwar My Faruuq ce? Zaunar da Zubaidaa Mum tayi Kafin ta ce "Ki kwantar da hankalinki ba budurwarsa ba ce asali ma ƙanwa ya ɗauketa. Nan ta sanar mata yadda suka haɗu.
Tuni idanuwanta suka kaɗa jawul. Ta ce, "Matsiyata ne fa, kuma talakawa fa Mum me yasa Faruuƙ ya cika kwashe-kwashe? Duk yadda aka yarinyar nan sonta yake kuma wallahi ba zai sameta ba, nice zai aura ba wata ba." Fuu! ta tashi tayi ciki.
Mum tsaki taja Zubaidaa har yanzun ba ta da hankali, wallahi bayan wasiya aka bari akan auransu, da babu dalilin da za ta yadda ɗanta ya auri wannan ballagazar yarinyar, sam ba ta da natsuwa da kamun kai, me ake da me irin halin Zubaidaa gashi shi kansa Faruuƙ baya son Zubaidaa, ita dai bata san yadda za a yi wannan cakwakiyar ba.
Bayan ya sauketa bai samu shiga ba saboda sallah da ake kira masallaci ya wuce ita kuma Sakinaa ta shiga gida, Umma alwala take don haka ita ma alwalar tayi bayan sun idar da sallar, ta nuna mata kayan da Mum ta bata, da saƙonta na gaisuwa.  "Shi ne daga baki abu ki ka karɓo?"
"Wallahi sai da na ce ta bar shi taƙi shi ne Hamma Umar ya amso." Umma ba ta kuma cewa komi ba.
Bayan isha'i tare suka shugo da Abba, nan Umma ta nuna masa kayan sukayi wa Umar godiya ya ce, "Haba dai sai ka ce wani abu don Allah ku daina mini godiya mun riga fa mun zama ɗaya, jini ɗaya kuma dangin juna."
Sosai ake daru a gidansu Umar akan auransa da Zubaidaa ya ce Shi ba ya son ta, nan fa iyaye aka haɗ daman Familynsu yawa ne dasu,(Akwai tarihi a gaba kaɗan.) Yayun Dad ɗin shi suka ce wallahi bai isa ba mahaifinsu ne yabar wasiya kuma daman can su auran zuminci su ke, kowa da abinda yake cewa Dad ya dun ga rarrashinsa akan ya amince.

Ya ce, "Zan amince Dad amma sai dai idan za a ba ni Sakinaa domin ban taɓa son  wata mace a duniyata ba irin Sakinaa wallahi ina ƙaunarta please Dad ka naimar mini auranta, ni dai burina a ba ni ita ko da ba yanzu za a yi auren ba."
Haka Dad yasa mi Malam Abdullahi da maganar, murmushi ya yi ya ce, "Ummaru yaron ƙyirki ne ni kaina zan so haɗa zuria da shi domin a kwai yaro mai kamala ta ko ina, ni na ba shi Sakinaa kuma na san ita ma za ta so shi duba da shaƙuwar da take tsakaninsu, amma ina so ya yi haƙuri har ta kammala Secondary sai ayi auren don haka kar ya da mu yanzu ya auri 'yar uwarsa." Nan fa Dad da Yayunsa suka yi ta godiya.
  Murna da farin ciki gurin Umar kamar me, nan aka fara shirin aurensa da Zubaidaa
  Yanzun su Sakinaa sun shiga ss2, kamar kullum suna haryar dawowa gida ita da Zaliha za su tsallaka titi kenan, wata mota ta rugo a guje sauran kaɗan tabi takansu saboda tsabar tsoro rungume junansu su kayi gabansu na bugawa, jin anja wani wawan burki suka dago a gigice, shi kuwa da ke cikin motar da sauri ya wani fito cikin masifa ya ce, "Ku waɗanne irin wawanyen yara ne? Wallahi da na bige ku na buge banza babu abinda za a yi, kuna tafe ba ku kallon gaban daƙiƙan yara kawai....

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUku
#LabarinSakinaa
_Gawurtattu uku 2014_

WANKA DA GARI...

©UmmuAffan

*Book 1 Page 7-8*

Ina kuke mata? Mata nake magana waɗanda suka amsa sunansu na mata ba muna mata ba! Kaya ne masu inganci waɗanda zai mai rabo ke samu. Ki buɗe bakin aljihu Hajiyata kiyi gyara da ingantattun kayanmu na GHT muna da.
Royal jelly-karin Niima jiki yayi kyau yyi sulbi kamar tawarda.
Akwai Garlic oil _maganin infection sadidan ga tightening da yke ka sa skin kyau sa namiji sunbatu.
Muna da Ganoderma reishi _xai ciccciko Miki da gaba ya motso d shaawa ya matse mace gam Yana gigita maxa.
Sannan akwai Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara

ya gyra skin yyi fresh.
Ba anan muka tsaya ba muna da irin su Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Da su Longzit-matan da suka Kai shekaru 40 Niima y fara karanci a jikin su ku Sha longzit ku bn labari.
Ga Panicept_duk wani ciwon Kashi da gabobi in Sha Allah matsala t kau.
Kuma akwai Sto care_ina masu ulcer duk karfin ulcer in Sha Allah xai magance masu shekara da shekaru Basu Yi axumi b sun gwada sun fara axumi ynxu.
Da Female _masu matsalar alada , infection,rikecewar jini matsi duk wata harka t gaban mace in Sha Allah.
Duk abin da kake buƙata zaka samu daga GHT sayen nagari mai da kuɗi gida kai tsaye kayi wa wannan number mgn domin haɗaku da sha yanzu magani yanzu wato Maman Amal GHT 08104335144

Shahararru goma a duniyar kayan mata Maman Zee ƙamshi and Kayan mata, duk wasu nau'i na kayan mata na gargajiya da na zamani gumba tsumi tabaje zuma masu ƙyau da inganci ku nemi maman zee ƙamshi an kayan mata a number kamar haka 0806 384 5136 Tana Bauchi tana aika kayanta gari-gari Ƙasa-ƙasa. Sayen na gari mai da kuɗi gida.

*Masu buƙatar ɗaura musu tallah suyi mgn cikin farashi mai sauƙi.* A saman rubutu ko a ƙasa ko wanne da farashinsa. Na gode.

...Cikin tsananin fusata Sakinaa ta ɗago ta kalle shi suka haɗa ido kuwa, da tsiwa ta ce, "Aikin banza taka wuƙar zakara kawai, kai da ka ke tuƙin kai baka kallon masu tsallakawa ne, ko kai makaho ne? Ko kuwa titin naka ne? Wallahi da ka bige mu ba ka bige banza sai an ɗaukar mana mataki, da har zaka fito kana wata fafarka ta banza."
Ido kawai ya zuba mata zuciyarsa na harbawa, lokaci ɗaya yaji yarinyar ta tafi da imaninsa, ganin taja hannun Zaliha za su wuce ya sa shi yin saurin shan gabansu.
Idanuwansa akan Sakinaa ya ce, "Kuyi haƙuri ban san ku ɗin na musamman ba ne. Tabbas na gane laifina ne amma hakan ba zai kuma faruwa ba."
Wata muguwar harara ta ban ka masa, Kafin a matsagaitan mintoci ta ƙare ma sa kallo, fari ne yana da tsayi kaɗan ba za a kira shi dogo ba amma shi ba gajere ba ne tsaka tsakiya, yana da baƙar suma a kan sa ya yi askin nan irin na samari 'yan kwallo an aske gefe sannan an bar wata cinkum a tsakiya, ba laifi shima yana da kyau daidai misali, sai dai leɓensa sun yi duhu alamar yana shan sigari. Shadda ce a jikinsa ɗinkin da samari ke yayi, cikin mintuna biyu Sakinaa ta ƙare ma sa wannan kallon
Taɓe baki tayi domin ko kwatar Hamma Umar ɗinta bai kai ba, sannan ita fa a rayuwarta bata wani ƙaunar farin namiji sosai, duk da take da duhu tafi son baƙin namiji ko wankan tarwaɗa, sake magana ya yi a karo na biyu.

"Please ku zo na rage muku hanya na ga ranar nan kamar tana damunku." Sakinaa tayi saurin cewa.
"Muka sanar maka? Ka ga malam don Allah ja ƙafarka ka ba mu guri, ba ma gayyar soɗi." Ta ƙarasasa maganar tare da murguɗa ma sa ƙaramin bakinta, bin bakin ya yi da kallo cike da sha'awa don shi yana son mace me tsiwa haka nan daga kallo ɗaya da ya yi wa Sakinaa yaji duk duniyar nan baya da abin so sama da ita, wata irin kaunarta ke fuzgarsa.
Yadda yake kallon Sakinaa haka Zaliha ke kallonsa, domin kallo ɗaya ta ma sa taji ya tafi da duka zuciyarta, ba ta taɓa soyayya ba, hasalima dukansu biyun ba su da samari, tana kallon gayen nan taji ya mata kuma zata iya aurensa.
Sakinaa taja hannunta, "Kin ga Zaliha zo mu wuce wannan ba shi da aikin yi." Riƙe hannunta Zaliha tayi gam alamar ta tsaya, kallonta tayi cike da mamaki ta ce, "Haba Sakinaa ya gane kuskuransa ya ba mu haƙuri don Allah mu hakura mana kin ga rana ta ishe mu tunda ya ce zai rage mana hanya don Allah kizo mu shiga, tunda babu ƙyau mayar da hannun ƙyauta." Da sauri ya ce, "Yawwa ƙanwata na gode gaskiya kina da saukin kai kin burge ni." Murmushi tayi tare da far da ido, cikon iyayi ta ce "Nima na gode."
Ba domin Sakinaa taso ba haka suka shiga motar. Zaliha ce gidan gaba Sakinaa daman baya ta shige, ba haka ya so ba amma ba shi da yadda zai yi. Sun fara tafiya ya kalli Zaliha tare da kallon Sakinaa ta madubi da ke kallon hanya, murmushi ya yi yarinyar na burgesa.
"Sunana Mubarak Sani Gata. Kuma yana da kyau naji sunanku."
Zaliha tayi fari da ido ta ce, "Wow nice name."
"Na gode ƙanwata."
"Ni suna na Zaliha Shehu ƙawata sunanta Sakinaa Abdullahi."
"Da kyau, manyan sunaye masu daraja." "Mun gode." Zaliha ta furta. Tambayar da ya yi unguwarsu ta sanar ma sa suka kama hanya.
Daidai ƙofar gidansu Sakinaa ya yi parking yana tsayawa ta fice da sauri ta shige gida Zaliha da Mubarak suka fito ta ce, "Am kayi haƙuri wallahi ƙawar tawa ni kaɗai nasan kanta." Murmushi ya yi.
"Kar ki da mu ai ƙawar taki mai tsada ce." Baban Zaliha ya buga addu'a take kar Allah yasa Mubarak ya ce Sakinaa yake so sai ita amma sai ji tayi yana cewa "Wallahi Zulaihat kallo ɗaya nayi wa ƙawarki naji duk duniya ba wacce nake so sama da ita, don Allah ki taya ni neman soyayyar ƙawarki."
Ƙirjin Zaliha babu abinda yake sai bugawa, yana ba da wani irin sauti mai ƙara, murmushin yaƙe tayi, "Kar ka da mu Mubarak, sai dai Sakinaar ce a kwai tsiwa, amma zan taya ka in sha Allahu."
"Yawwa ƙawarmu na gode sosai. Nan ne gidanku duka?"
"A'a nan gidansu Sakinaa ne." Da hannu ta nuna ma sa nasu gidany.
"Ok na gode sosai Zulaihat."
"Babu komai." Kuɗi ya bata taƙi amsa, ganin ya dage ta amsa sannan suka yi sallama ya wuce, bin motarsa tayi da kallo, daga bisa ni ta wuce gidansu jikinta a matuƙar sanyaye.
Suna zaune take sanar da Sakinaa duk abinda ya faru, tsaki taja ta ce, "Yana son wa? Wai ni?" Gyaɗa kai Zaliha tayi alamar
"I."
"Hmmm idan ma ni ce gara ya yi haƙuri domin ni ba aure ba ne a gabana, hasalima karatu zan

yi yanzun nake ss2 ban kammala Secondary ba balle naje jami'a. Don haka ya je ya nemi wata, kin ga Abbana ma ya mini faɗan kar na kula kowa haka Hamma Umar ya ce kar na kula kowa nasa karatuna a gaba don haka sai ki ba shiaɗ haƙuri, ke nifa ma mutumin nan bai mini ba wallahi tunda na kallesa na san baya cikin tsarina, fuska kamar jan ƙosai, kin san fararen maza ba sa cikin jadawalina." Ota dai Zaliha ba ta ce komai ba sai bin ta da ido take.

Yana parking a babban harabar gidan ya fito da sauri A Parlour ya iske Hajiyarsa da ƙannansa, jikin Hajiyar ya faɗa yana sauke a jiyar zuciya. Sannu kawai take ma sa tana shafa kansa, Ƙannansa suka ma sa sannu.

Hajiya ta ce, "Mubarak lafiya yau na gan ka wani iri haka?" Sumar kan sa ya shafa tare da fesar da huci mai ɗumi ya ce, "Hajiya yau na samar miki surika." Shewa ta zuba haka sauran ƙannansa Safah da Marwah sai Laurah.

Tuni suka dawo jikinsa Hajiya ta ce,

"Wannan wacce mai sa'ar ce ta sami santalelan yarona ɗan zamani son kowa ƙin wanda ya rasa, sannan ɗan Hajiya?" Yaƙe ya yi ya ce, "Uhmm Hajiya yarinyar fa na lura ba ta sona ni ne kawai ke haukana, kuma wallahi idan na rasata daidai yake da rasa numfashina." A harzuƙe ta ce, "Wace ce wannan? Wane ne ubanta a garin nan? Da har za ta ce ba ta sonka?

Uban waye ubanta a ƙasar nan da har zata ce ɗana son kowa ga kuma kwalisa dukiya mulki ga uwa uba kyawu." Larah ta ce, "Kai Hajiyarmu duk irin wannan washi haka, shi so fa ba ruwansa da kyawu ko kuɗi da sauransu." Harara Hajiya ta zuba mata ta ce, "Matan zamanin nan me suke so idan ba kyakkyawan saurayi mai 'ya'yan banki bugun Abuja ba?"

Mubarak ya ce, "Duk ba wannan maganar ba, ni dai Hajiya a nemo mini soyayyar Sakinaa kawai nake buƙata, kuma ko ta halin ƙaƙa ne."

"Ta ya?" Larah ta tambaya.

Hajiya ta ce, "Larah ko ta halin ƙaƙa ne ina ruwanki wai? Tashi ki bar gurin nan domin duk a yarana ke ce ki ka banbanta da sauran, sai ka ce ba ni ce uwarki ba. Ni Hajiya Amina naci dubu sai ceto."

Miƙewa ta yi, "Shi ke nan bari in ba ku guri, amma ina son ku sani shi so na gaskiya ba ruwansa da kuɗi ko ilmin, mutum da kyawunsa Allah yana da sa so ne a duk zuciyar wanda ya yi niyya."

Tana gama wa tayi wucewarta suka bita da tsaki Hajiya kallon ɗan nata tayi mafi soyuwa a zuciyarta wato Mubarak ta ce, "Yarona faɗa mini sunan ubanta a faɗin ƙasar nan ko 'yar wace ce dole ta so ka, kai ko da shugaban gasa ne ubanta kuwa."

Kallon Hajiyar tasa ya yi wacce a saninsa ta tsani talaka kowa ye, bata hurɗa da ƙananun mutane ya ce, "Hajiyata Sakinaa ba kowa ba ne ubanta, hasalima yarinya ce ƙarama bata wace 16years ba, ba kowa ba ne ubanta sai matalauci, sai dai ina son ki san wani abu guda, idan ban same ta ba wallahi mutuwa zan yi."

Kallon ɗan nata tayi cikin so da kauna, wannan wacce irin jarabawa ce ɗan ta zai kamu da son 'yar matsiyata? Amma ba tayi ƙasa a gwiwa ba ta ce, "tashi muje gidan." haka ta tasa shi a gaba har ƙofar gidan a tsiya ce ta kalli gidan ita unguwarma sam bata mata ba,

"Yanzu Mubarak ka rasa gidan da zaka ɗauko aure sai a unguwar matsiyata, don Allah kabar wannan maganar 'yar wannan akurkin gidan za ka ce kana so? Gabaɗaya yankin nan bai mini ba."

Ya ce"Hajiya kina so ki ra sani ko? To ina son ki sani 'yar wannan akulkin gidan ce farincikin ɗan ki, tunda dai wanka da gari ba shi maganin yunwa sai an sha." Numfashi taja cike da ƙyanƙamin

layin.
Fita tayi ta nufi cikin gidan, Umma na zaune kan kujera 'yar tsugunnau tana firfita wutar itace a mirhu. Sakinaa kuwa ta fito kenan cikin shirin islamiyya Abba yana gareji.
Ko sallama Hajiya ba ta yi ba, sosai suka tsorata. Umma har da salati, kallonta Hajiyar tayi cike da kyama ta ce, "Gurin Sakinaa nazo." Daga Sakinaar har Umma ido suka zuba mata cike da mamaki, duk a zatonsu ba musulma ba ce jin ba tayi sallama ba, kuma ko hijabi ko gyale babu a jikinta kuma sai su kaji tayi hausa.
Cike da takaici Umma ta ce, "Malama lafiya gidan musulmai fa ki ka shugo." Harara Hajiya ta ban ka mata ta ce, "Ai ina sane sallamar ce bata da ce da na muku ba, domin baku isa ba shi ya sa."
Kallonta suka ci gaba da yi ta sake cewa tambayar Sakinaaa tazo nema. Ganin kallon da Umma take aika wa yarinyar da ke tsaye a gurin yasa Hajiya ta ga ne ita ce Sakinaa, kama hannuwanta Hajiya tayi suka fita waje, Umma kuwa saboda mamaki kasa cewa uffan tayi sai raka su da ido.
Hajiya ba ta tsaya da Sakinaa ko ina ba sai bakin mota. Mubarak na ganinsu ya fito yana washe baki, tana ganinsa gabanta ya buga da ƙarfi har lokacin Hajiya bata saki hannun Sakinaa ba. Mubarak zubawa Sakinaa ido ya yi ita ma ta zuba ma sa ido.

Yayin da Hajiya ke ta wasu 'yan surkullenta da hannun Sakinaa lokaci guda, Sakinaa taji kan ta ya mata wani nauyi lunshe idanuwanta ta fara zuwa wani lokaci tayi luuuw zata faɗi da sauri Mubarak ya ruƙota jikinsa. Hajiya ta ce, "Aiki ya yi kyau shi ya sa nace maka ko ɗiyar shugaban ƙasa ka ke so zaka samu in dai ni ce uwarka." Murmushin farin ciki ya yi ya ce, "Shi ya sa nake ƙaunarki Hajiyata, tsafinki yana aiki kobme nake so kina mini gaskiya naji daɗon gadon nan da kika yi na mahaifinki." Murmushi kawai tayi ta dafa saitin zuciyar Sakinaa wajen minti biyu sannan ta dafa saitin zuciyar  Mubarak. Dariya su ka yi gabaɗaya sannan ta bubbuga jikin Sakinaa nan take ta farko zata kurma ihu Mubarak ya yi saurin ɗaura hannunsa saman leɓenta, nan take tayi shuru sai ta zuba musu ido.
Hajiya ta ce, "Sakinaa ina son ki shiga cikin zuriata hakan ba zai samu ba sai kin amince da auren ɗana Mubarak ko me ki ke so za muyi miki abinda ma yafi wanda iyayenki ke miki."
Shuru tayi tana kallonsu gabanta ya tsananta bugawa. Mubarak ya ce"Ina ƙaunarki Sakinaa kema kina so na?" A hankali ta buɗe baki za tayi magana sai suka jiyo muryar Zaliha na kiran Sakinaa.
Daidai ƙarasowar Zaliha Sakinaa ta buɗe baki ta ce.
Ta ce, "Ina sonka nima kuma zan aure ka." Hajiya da Mubarak suka kalli juna su kai murmushi. Zaliha kuwa dafe ƙirji tayi tana kallon Sakinaa kafin ta ce "Sakinaa lafiyarki kuwa?"
Kallonta Hajiya tayi ta ce, "Wace ce ke?" Cikin rawar murya ta ce "Ni ƙawarta ce." Hajiya zatayi maganantu sai ga Abba shi da Hamma Umar gurin, suka ƙara so har da Umma, wacce jin Sakinaa shuru ta fito domin ta ga ko lafiya.
Abba ya ce, "Sakinaa Zaliha me ku ke a nan?" Shuru dukansu su ka yi suna kallon-kallo, a nan Umma ta sanar masa abinda ya faru, cike da mamaki ya kalli Hajiya kafin ya kalli Sakinaa ya ce, "Zo ki wuce." Kasa ɗaga ƙafarta tayi tana son bin umarnin Abbanta amma ta kasa.
Murmushi Hajiya tayi ta ce, "Kai malam ka ke kowa, to bari kaji ɗana ne gashi nan Sunansa Mubarak, ta nuna sa taci gaba da cewa "shi ne ke son 'yar ka bayan ma ya nace me za mu yi

da 'yarka yana sonta kuma cikin satin nan nake son a ɗaura musu aure."
Cike da tashin hankali suka bita da kallo Abba zai yi magana Hamma Umar ya ce, "Wannan wanne irin hauka kike, ke kuwa matar nan kina da cikakken hankali da tunani? A wanne garin mahaukatan ake haka?" Abba ya ce, "Gaskiya da dai sauƙi Ummaru, to ina son ki sani bazan ba ɗanki 'yata ba domin daga ke har ɗan naki ban ga kuna da alamun tarbiyya ba, ke barama kiji me kankat nawa 'yata miji lokaci kawai nake jira a ɗaura mata aure."
Sakinaa ce ta kalli mahaifinta a rikice ta ce, "Ka ba da ni kuma Abba? Ni dai ban so wannan nake so." Ta nuna Mubarak daga Abba Umma Hamma Umar Zaliha ido suka kyalalo suna kallonta.
Hajiya da Mubarak kuwa murmushi suka yi, Hajiya ba ta ce komai ba ta kama hannun Mubarak suka koma mota, bayan sun shiga Mubarak ya ce, "Hajiya ya na ga haka?" ta ce "kai dai ja mota mu tafi Sakinaa da kan ta zata nemeka."
"Amma ban sanar da ita inda nake ba."
"Kai dai muje gobe zaka dawo....
08104335144

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUku
#LabarinSakina
_Gawurtattu uku 2024_

WANKA DA GARI...

©UmmuAffan

*Book 1 Page 9-10*

Ina kuke mata? Mata nake magana waɗanda suka amsa sunansu na mata ba muna mata ba! Kaya ne masu inganci waɗanda zai mai rabo ke samu. Ki buɗe bakin aljihu Hajiyata kiyi gyara da ingantattun kayanmu na GHT muna da.
Royal jelly-karin Niima jiki yayi kyau yyi sulbi kamar tawarda.
Akwai Garlic oil _maganin infection sadidan ga tightening da yke ka sa skin kyau sa namiji sunbatu.
Muna da Ganoderma reishi _xai ciccciko Miki da gaba ya motso d shaawa ya matse mace gam Yana gigita maxa.
Sannan akwai Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.

Ba anan muka tsaya ba muna da irin su Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Da su Longzit-matan da suka Kai shekaru 40 Niima y fara karanci a jikin su ku Sha longzit ku bn labari.
Ga Panicept_duk wani ciwon Kashi da gabobi in Sha Allah matsala t kau.
Kuma akwai Sto care_ina masu ulcer duk karfin ulcer in Sha Allah xai magance masu shekara da shekaru Basu Yi axumi b sun gwada sun fara axumi ynxu.
Da Female _masu matsalar alada , infection,rikecewar jini matsi duk wata harka t gaban mace in Sha Allah.
Duk abin da kake buƙata zaka samu daga GHT sayen nagari mai da kuɗi gida kai tsaye kayi wa wannan number mgn domin haɗaku da sha yanzu magani yanzu wato Maman Amal GHT 08104335144

Shahararru goma a duniyar kayan mata Maman Zee ƙamshi and Kayan mata, duk wasu nau'i na kayan mata na gargajiya da na zamani gumba tsumi tabaje zuma masu ƙyau da inganci ku nemi maman zee ƙamshi an kayan mata a number kamar haka 0806 384 5136 Tana Bauchi tana aika kayanta gari-gari Ƙasa-ƙasa. Sayen na gari mai da kuɗi gida.

*Masu buƙatar ɗaura musu tallah suyi mgn cikin farashi mai sauƙi.* A saman rubutu ko a ƙasa ko wanne da farashinsa. Na gode.

A ɓangaren su Abba kuwa Sakinaa na ganin su Mubarak sun tafi ta saka kuka, da yaja motar kuwa bin bayansu tayi Hamma Umar ne ya kamota, kuka take sosai da haka suka shiga cikin gida.
Umma saboda takaici rufe Sakinaa tayi da bugu Abba kuwa zurum ya yi yana tunan. Bai taɓa hasaso ko tunanin Sakinaa za tayi haka ba, ɗan yau kenan da baka shaidar shi, sai ya baka kunya a idon duniya. Yanzu ga shi ya ɗau alkhawarin bai ma Umar ita ga shi za ta ba shi kunya. Babu wanda ya kai Umar tashin hankali don suna shugowa ya musu sallama ya tafi gida kawai. Allah ne ya kai sa gida lafiya domin gudun da yake ya wuce ƙa'ida ga shi baya cikin haiyacinsa, bai san ma ya aka yi yazo gidan ba, domin tunaninsa fita ya yi a ƙwaƙwalwarsa, yana parking ya fito ko motar bai iya rufewa ba. Yana shiga Parlour kuwa ya zube yana wani irin numfashi da kakarin amai.
Su Dad daga sama suka farajin kakarin aman sa sun ji tsayuwar motarsa amma suka ji shi shuru bai hawo sama ba. Da sauri suka fito ai hango sho su ka yi zube yana amai, da sauri suka ƙarasa, tuni Mummy ta ruɗ nan ta fara kuka ganin aman jini yake. Dad ma hankalinsa ya tashi rungumesa ya yi yana tambayarsa abinda ya faru, ya kasa magana sai saitin zuciyarsa da yake nuna musu zuwa can ya yi luww! Ya zube jikin Daddy a sume.
Mummy ta saki wani rikitacciyar ƙara mai haɗe da sautin kuka ta kurma ihuw. Daddy ne ya yi ƙarfin halin ɗauko ruwan sanyi ya zuba masa amma ko ɗan yatsansa bai yi motsi ba, nan fa

suka sake ruɗewa, Da ƙyar Daddy ya iya cicciɓar Umar don shiɗin cikakken namiji ne ga tsayi ga shi kuma ƙaƙƙarfa, sai da Mummy ta riƙe ƙafafuwansa shi kuma ya riƙe can wajenuwar jikin da kai sannan suka nufi harabar gidan, cikin mota suka saka shi Mummy ta shiga bayan tare da ɗaura kansa bisa cinyarta tana ta kuka shi kan sa Daddy ƙarfin hali yake da haka yaja motar suka nufi asibiti.
Suna isa aka ɗauko irin kujerar nan ta tura marasa lafiya a kai aka ɗaurasa suka nufi ciki, nan fa Lokitoci suka fara ba shi taimakon gaggawa.
  A gidansu Sakinaa kuwa rigima sabuwa domin haƙiƙancewa tayi ita fa Mubarak take so. Umma dukanta take amma bakin yaƙi mutuwa don Umma ba ta da haƙurin irin haka.
"Don ƙaniyarki mu muka haifeki ba ke ki ka haifemu ba, da zaki ce ba zaki bi umarninmu ba." Cikin kuka ta ce, "Wallahi Umma ko kashe ni zaki yi bazan daina ce miki Mubarak nake so ba." Saitin bakin Umma ta buga nan kuwa ya fashe Sakinaa ta saki wani gigitaccen kuka duk da haka ba ta fasa cewa Mubarak take so ba.
Abba ne ya jenye Umma daga bugun da takewa Sakinaa ya ce, "Rabu da ita Hadiza kanta tamawa mu dai take gayawa irin waɗannan kalaman ko, duk wanda yaƙi ji ai ku to ba zai ƙi gani ba, duniya ce ta ishi kowa riga da wando."
Bayan wucewarsu Zaliha ta din ga kallon Sakinaa  rai ɓace ta ce "Yanzu Sakinaa saboda wani banza can ki ke wa iyayenki wannan cin mutuncin? Abinda baki taɓa ba, duk gatan da iyayenki ke miki ki rasa da abinda zaki saka musu sai na butulcewa ina ji miki tsoran wataran ki girbe abinda kika shuka."
Miƙewa Sakinaa tayi cike da bala'i.
"Ina ruwanki, me ya shafeki? Nayi ɗin iyayenki ne ko nawa? Daƙiƙiya wawiya kawai." Zaliha ta ce, "Kai ni ki ke zagi haka Sakinaa? Ai gaki nan babbar daƙiƙiya marajin maganar iyayenta, akwai wawiya da ta fiki?" Ai kafin ta rufe baki Sakinaa cikin zafin nama ta kai mata bugu a baki Zaliha ma ta ce ba ta isa ba nan suka fara danbe na bala'i.
Sai da Abba ya shugo ya raba su ya ce, "Zaliha rabu da ita ai abinda mutum ya shuga shi yake girba, tayi lokacinta ne, wata rana sai labari, waɗanda suka yi abin da yafi nata ma yanzu ina suke?" Haka ya kama Zaliha suka fita, Sakinaa kuwa ko ajikinta wai an tsikari kakkausa, zama tayi tana zan tsaki Mtsuw ta ce A bayyane "Wallahi ba wanda ya isa ya raba ni da Mubarak ina son sa kuma sai na aure shi."
A can asibiti kuwa an samu Umar ya farfaɗo sai dai da sunan Sakinaa a bakinsa, ita kawai yake kira Likita ya sanar da Daddy tabbas a kawo Sakinaa domin sun masa allurar bacci suna so da ya farko ya ganta idan ba haka ba kuwa akwai matsala. Hankalin a tashe Daddy ya nufi gidansu Abba, ya sanar masu duk kan abinda ya faru. Umma kuka kawai ta fara Abba ya fara sallallami hawaye kwance a idonsa.
  Ɗkin Sakinaa Abba ya nufa, kwance ya isketa tana hawaye tana ganinsa ta juya masa baya cike da mamaki Abba yake kallonta kafin ya ce, "Sakinaa Umar yana asibiti babu lafiya shi ne na ce ki shirya muje."
Turo baki gaba tayi cikin halin ko in kula ta ce, "Ni Abba babu inda zani." Buɗe ido ya yi yana kallonta kafin ya iya furta. "Sakinaa ni mahaifinki Mamal Abdullahi Bakanike ki ke faɗawa wannan maganar mai zafi da ɗacin furzarwa, kina da hankali kuwa?"
Banza ta masa tana ƙunƙunai abin ya ɓata wa Abba rai bai san lokacin da ya kwasa mata mari ba, riƙe kuncinta tayi tare da sakin wani rikitaccen kuka ta ce, "Ni wallahi babu inda zan je."

Jin kukanta Daddy da Umma suka shugu. Daddy da bai san wainar da ake toyawa ba ya yi tambaya, nan suke sanar ma sa duk abinda ya faru, kallonta ya yi "Sakinaa me ke damun ki iyaye ba abin wasa ba ne, sam."
Ko ƙala ba ta ce ma sa ba, sai harare-harare da take. Daddy ne ya ce, "Tunda ba za ta ba shi ke nan." Lallaɓa ba irin wacce Abba baiwa Sakinaa ba taƙi, mai haƙuri bai iya fushi ba haka ya rufeta da bugu amma ko gezai ba tayi ba, akan bata zuwa. Daddy ne ya bawa Abba haƙuri sannan suka tafi duka asibitin.
Ko da Umar ya farfaɗo ya ga su Abba kuka ya saka ya ce, "Abba ka mini alk'awarin zaka ba ni Sakinaa don Allah ka bata haƙuri kar ta guje ni ita ce FARIN CIKINA."
Abba da Umma me za su yi ba kuka ba. Abba ya ce, "Umar tabbas na maka alƙawarin baka Sakinaa amma ban taɓa tunanin ko kawo za taƙi bin umarni ni ba ɗan yau ne ka haifesa amma baka haifi halinsa ba tabbas Sakinaa ta ba ni mamaki amma duniya ce ta isheta riga da wando har da zanin ɗaurawa."
Hawaye Umar yake yana danne saitin zuciyarsa tabbas Allah ne ya dasa masa ƙaunar Sakinaa ba shi ne ya sawa kan sa ba.
Haka Umar ya yi jinyar kwana biyu yaji jiki sosai, amma Sakinaa ba ta zo ba, Zaliha tana zuwa tare da Umma ta tausayawa Umar sosai har kuka take idan suka je.
Bayan sun koma gida. Daddy ya ɗauki Mummy da Umar suka je gidan Abba, don Umar ya matsa yana son ganin Sakinaa. Ranar da suka je suka iske durama domin Mubarak ne yazo Abba yanawa Sakinaa magana taƙi ji wai lallai sai tabi Mubarak, wasu zafafan hawaye ke zubowa a fuskar Hamma Umar, ganin yadda Abba yake dukan Sakinaa yasa yaje ya riƙeshi ya ce, "Please Abba rabu da ita indai don ni ne wallahi daga yau na haƙura da Sakinaa ka bata wanda take so, ba zan so na auri Sakinaa amma zuciyarta tana gurin wani ba, na haƙura Abba."
Gabaɗaya zuba ma sa ido su kai cike da tausayi kowa na hawaye, ɗaga Sakinaa ya yi ya ce, "Sorry Princess Abba zai baki wanda ki ke so, kwantar da hankalinki ƙanwata."
Daddy ya ce, "Allah na gode maka da ka ba ni yaro adali wanda yasan ya kamata, tabbas abinda kayi shine daidai Umar masoyin gaskiya shine ke iya sadaukar da farin cikinsa domin farin cikin abinda  yake so, wannan shine so na haƙiƙa wanda babu gauraye ko algus a cikinsa."
Abba ya dafa Umar ya ce, "Allah ya maka albarka Umar tabbas Sakinaa ta ba ni kunya, amma kan ta tabawa ina roƙon Allah ya baka juriya da hakurin rashinta ya kuma zaɓa maka mata ta gari." Hawaye ne suka gangaro a fuskarsa ya ce "Amin Abba."
Juyowa Abba ya yi ya kalli Mubarak Ya ce, "Ina so ka turo iyayenka yau ɗin nan su kawo sadaki kawai nake buƙata dubu Ashirin gobe Juma'a a masallaci za a ɗaura muku aure. Ba na ƙaunar wannan butulun yarinyar ta ƙara wuce gobe a gidana."
Ai daga Sakinaa har Mubarak murmushi a ka ga suna yi. Mubarak ya ce, "To na gode bari naje na sanar musu." Ya kalli Sakinaa suka sake yin murmushi ya fice. Dukansu kasa magana su ka yi abin ya ba su al'ajabi haka Sakinaa ta wuce ɗakinta cikin murna har da tsalle.
Daddy suka musu sallama jiki a sanyaye suka fita. Abba da Umma ba wanda ya iya magana dukansu sun yi jigum-jigum.
Zaliha ce ta nufi ɗakin Sakinaa wacce ke ta faman haɗa kayanta waje guda na tafiya ɗakin miji, don har a zuciyarta ta ƙosa safiyar gobe ta waye.
Kallonta tayi galala ta ce, "Sakinaa wai kan ki guda kuwa?" Ba ta waigo ba ta ce, "To duba da

ƙyau dai, idan kuma na haɗa shi da naki ne to?" Zaliha ta riƙe baki cike da mamaki kafin ta ce, "Sakinaa zaki yi kuskure babba kuwa kinƙi bin umarnin iyayenki ba abu me sauƙi ba ne, ki dawo haiyacinki Sakinaa. Tsuwww Sakinaa taja tsaki ba ta kuma tanka mata ba. Zaliha ta zuciya sosai ta ce, "Sakinaa tabbas zaki ga ne kuranki, masoyinki na haƙiƙa Hamma Umar sai Allah ya saka masa haka iyayenki ma."
Cikin tsananin fushi Sakinaa ta ce, "Wai Zaliha ina ruwanki ne? Iyayenki ne ko nawa? Idan kin ji haushi ki auri Hamma Umar ɗin mana.
"Ni bazan auresa ba, amma ina son ki sani sai na rama masa abinda ki ka masa ni Zaliha Shehu nayi alkhawarin sai nasa kin yi da nasanin abinda kika yi, daga ke har wannan shegen Mubarak ɗin." Kuka Sakinaa ta kama "Allah ya isa tunda ki ka kira sa, shege wallahi da ki zagi Mubarak gara ki zage ni shi ba shege ba ne da ubansa."
Baki da hanci da kuma kunne sai ido Zaliha ta saki tana kallon Sakinaa a mamakance, nan take wani tunani ya faɗo mata anya kuwa Sakinaa cikin haiyacinta take? Domin biri ya yi kama da mutum abin ya yi yawa." Fita tayi amma tasa a zuciyarta ko ta halin ƙaƙa sai ta ceto ƙawarta daga wannan halin, sai ta nuna mata abinda tayi babban kuskure sai ta nuna mata zaki ko a dawa shi ne sarki.
Mubarak kuwa cike da murna ya shiga cikin gidansu, tun daga harabar gidan yake kwalawa Hajiya kira.
Da sauri Hajiya ta fito tana cewa "Mubarak lafiya kuwa?" Domin ta zaci ko wani abin ne ya faru da shi, jikinta ya faɗa yana cewa "Hajiya mun ci su da yaƙin, Abban Sakinaa ya ce a kai sadaki gobe za a ɗaura mana aure."
Wani irin shu'umin murmushi tayi "Wa ya faɗa musu barno gabas take? Daman me na faɗa maka?"
"Hajiya kizo muje kawai a kai sadakin." Murmushi ta kuma, wayarta ta ciro ta kira ƙaninta Buhari ta ce, "Kazo yanzun nan ina son ganinka."
Ba a yi cikakken awa ba sai ga shi bayan sun gaisa take sanar da shi kuɗin auren Mubarak za su kai kuma gobe ne bikin.
Cike da mamaki yake kallonta ya ce, "Kuɗin aure kuma Hajiya? Goben nan biki amma ba mu ji ba sai yau?"
"Abin ne yazo na gaggawa yanzu iyayen yarinyar mu ma suke sanar mana, ka ga indai maganar kuɗi ce mu ba mu da haufi, don haka ka tashi muje mu kai kuɗin." Zaro ido ya yi "Hajiya mu zamu kai kuɗin? Ina su Alhaji Sani da Alhaji Lawan ƙannan mahaifinsa? Ai su ya dace su kai komai dangin ubansa."
Harara ta banka masa ta ce, "Kasan dai ni da yarana ba shiri muke da su ba, don haka bazan bari su shaga maganar yarana ba yanzu kuɗi suke magana ko ba dangin uba?" Zai yi magana ta katse shi "Ka ga Buhari idan kai ma ba za ka je ba, ni kaɗai sai inje tunda ƙafa gare ni. Saboda yana matuƙar jin tsoranta yasa shi ammasawa da "To idan kin shirya sai mu wuce." Amma shi dai ai ya san da uba ake ado.
Mayafi da jaka ta ɗauko suka fita Mubarak ya kai su gidansu Sakinaa, bayan sun gaisa da Malam Abdullahi suka masa maganar sun kawo kuɗin auren ne.
Daga Umma har shi suka kalli juna cike da al'ajabi, to ya suka iya 'yarsu ce ta musu wannan kwashe-kwashen wai uwar yaro da kawo kuɗin auren ɗanta ba su taɓa gani ba. Ko a garin mahaukata.

Dubu ɗari biyu ta ba da ta ce, "wannan kuɗin nagani ina so, ta bada wasu ɗari biyar ta ce na sadaki ta bada ɗari uku ta ce na uwa da na uba. Harararta ita da kuɗinta Abba ya yi ya ce, "Ki kwashe abin ki ba su muke buƙata ba abinda kawai nake so dubu ashirin sadakinma don ya wajabta da bazan amsa ba.
Ta ce, "Shi ke nan, kayi wa kan ka, amma ba ma so ku kawota da komai ita kaɗai muke so."
Haushi ya cika Abba ya ce"Idan mun kawota da su sai ku zubda, sannan ya tashi ya fita.
Zuciyarsa na suya kamar an ɗaurata a tukumar tsure...
08104335144

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUuku
#LabarinSakina
_Gawurtattu uku 2024_

WANKA DA GARI...

©UmmuAffan

*Book 1 Page 11-12*

Ina kuke mata? Mata nake magana waɗanda suka amsa sunansu na mata ba muna mata ba!
Kaya ne masu inganci waɗanda zai mai rabo ke samu. Ki buɗe bakin aljihu Hajiyata kiyi gyara da ingantattun kayanmu na GHT muna da.
Royal jelly-karin Niima jiki yayi kyau yyi sulbi kamar tawarda.
Akwai Garlic oil _maganin infection sadidan ga tightening da yke ka sa skin kyau sa namiji sunbatu.
Muna da Ganoderma reishi _xai ciccciko Miki da gaba ya motso d shaawa ya matse mace gam Yana gigita maxa.
Sannan akwai Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Ba anan muka tsaya ba muna da irin su Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Da su Longzit-matan da suka Kai shekaru 40 Niima y fara karanci a jikin su ku Sha longzit ku bn labari.
Ga Panicept_duk wani ciwon Kashi da gabobi in Sha Allah matsala t kau.
Kuma akwai Sto care_ina masu ulcer duk karfin ulcer in Sha Allah xai magance masu shekara da shekaru Basu Yi axumi b sun gwada sun fara axumi ynxu.

Da Female _masu matsalar alada , infection,rikecewar jini matsi duk wata harka t gaban mace in Sha Allah.
Duk abin da kake buƙata zaka samu daga GHT sayen nagari mai da kuɗi gida kai tsaye kayi wa wannan number mgn domin haɗaku da sha yanzu magani yanzu wato Maman Amal GHT 08104335144

Shahararru goma a duniyar kayan mata Maman Zee ƙamshi and Kayan mata, duk wasu nau'i na kayan mata na gargajiya da na zamani gumba tsumi tabaje zuma masu ƙyau da inganci ku nemi maman zee ƙamshi an kayan mata a number kamar haka 0806 384 5136 Tana Bauchi tana aika kayanta gari-gari Ƙasa-ƙasa. Sayen na gari mai da kuɗi gida.

*Masu buƙatar ɗaura musu tallah suyi mgn cikin farashi mai sauƘi.* A saman rubutu ko a ƙasa ko wanne da farashinsa. Na gode.

Hajiya kuwa taɓe baki tayi aikin ɓul, inji tusa a ranta kuwa ta furta 'Wallahi can da su gada. Ku ne matsiyata kuma a haka zaku ƙare, matsiyatan banza kawai da ba ku san alkhairi ba, ko ina dai matsiyaci sunansa kenan.'
Washe gari Juma'a aka ɗaura auren Mubarak Tahir da Sakinaa Abdullahi a masallacin Juma'a bayan idar da salla. Umar da ƙarfi ya runtse idanuwansa lokacin da yaji ɗaurin auren, ji ya yi kamar an saukar da guduma a kan sa.
Da yake shi da Daddynsa sunzo ɗaurin auren. Abba ya kalle shi cike da tausayi, Allah ya gani yaso haɗa zuri'a da wannan natsattsen yaron, amma Allah bai nufa ba, ina ma ace yana da wata 'yar bayan Sakinaa, tabbas da ya wanke ma shi ruwan idaniyarsa da raɗaɗin da Sakinaa ta furza ma shi, amma ba komi yana ma shi addu'a Allah ya ba shi mata tagari wacce tafi Sakinaa a ko mi, ko da yake bikin shi da 'yar uwarsa Zubaidaa sauran sati biyu inji Daddynsa. Amma ya san ba wai yana ƙaunarta ba ne, idan ita ce alkhairinsa Allah ya tabbatar ma shi.
Mubarak ya fi kowa farin ciki haka aka gama ɗaurin aure lafiya, daga baya aka ɗum guma zuwa gida. Mubarak ya riga kowa isa gidan Abba, kamar yadda Abban ya sanar masa idan an ɗaura aure yazo ya tafi da matarsa.
Bayan sun iso, tare suka shiga ciki, UMAR Daman daga masallacin wucewa su ka yi gida shi da Daddy.
Umma na zaune tsakar gida ta buga uban tagumi tun lokacin da aka tafi ɗaurin auren take cikin damuwa ta rasa me ya sa ta tsinci kanta cikin rashin sukuni ko da yake dole a rina wai an saci zanen mahaukaciya mai rasa nasaba da wannan ƙaddararren auren da Sakinaar ta zaɓawa kan ta, tana jin zafi da ɗacin abinda Sakinaa ta musu haƙƙun.
Ita ma Sakinaa tun lokacin da taji Abban nayi wa Umma sallamar sai ya dawo take cikin farin ciki, yau za a aura mata abin sonta, murna ta dun ga yi daga bisani ta fara tattara komai nata, ta kintsa guri guda sai da tagama haɗawa kuma taji gabanta na faɗuwa sai ta kama kuka tana so taji tausayin iyayenta da Hamma Umar ɗinta amma zuciyarta na hanata, hakan yasa zazzaɓi

mai zafi ya rufeta, kwantawa tayi bisa katifarta tana rawar sanyi tana kuka sosai, a haka su Abba da Mubarak suka shugo.
Abba ya zauna kusa da Umma. Mubarak ya yi tsaye a kan su babu alamun tarbiyya ya ce, "Ina matata Sakinaa take." Kallonsa su kayi Abba ya yi ƙarfin halin cewa tana ɗaki don Umma ji take kamar ta shaƙesa ya mutu.
Ɗakin ya shiga da sauri ya yaye lilliɓin da tayi da zani ya ce, "Kinaata lafiya kuwa?" Hawaye ne kwance a idonuwanta "Ba na jin daɗi ne Mubarak zazzaɓi mai zafi ya rufe ni kuma ba na son rabuwa da su Um...."
Bai bata damar ƙarasawa ba ya rufe bakinta da nasa, ya ɗaki wani lokaci kafin ya sakar mata baki idanuwan nan nasa tuni suka sauya launi.
"Kar in sake jin kin faɗi hakan, yanzu ne za ki yi rayuwa mai daɗi da ni Kinaata, nayi alƙawarin jiyar da ke daɗi da saka nishaɗi. Ki man ta da kowa da komai kin ji."
Sake lafewa tayi jikinsa tana hawaye domin Abbanta da Ummanta na ranta, ɗaukarta ya yi kamar wata jariri ya yi waje da ita, suna fitowa ta fara ƙoƙorin sakkowa tana zullewa amma bai bata damar hakan ba saboda irin ruƙon da ya mata, "Abbana! Ummata" Abinda ta iya faɗa kenan ya fi ce da ita.
Su kuwa girgiza kai kawai su ka yi.
Kai tsaye wani asibiti mai zaman kansa ya nufa da ita, yana zuwa ya ce a ba ta gado a samata ƙarin ruwa hakan kuwa a ka yi, yana zaune bakin gadon inda ta sami bacci sakamakon allurar bacci da aka haɗa a ruwan, wayarsa ya ciro ya kira Hajiya ya sanar mata nan take ta aiko Laura ita da Direba suka taho musu da abinci domin a can gidan ba ƙaramin biki suke sha ba.
Sai bayan magrib ta farka jikinta ya mata sauƙi, taji ƙarfi alwala tayi tayi sallolin da ke kanta har isha'i da ake kira yanzu, bayan nan Mubarak da kan shi ya zuba mata abinci zaunawa ya yi a daddumar kusa da ita ya ɗaura kafafuwanta bisa cinyarsa da sauri zata zame ya riƙe ƙafafuwan, ita kuwa duk kunyar Laura ta isheta a hankali ta juyo ta kalleta gani tayi hankalinta ma baya kansu chating kawai take a wayarta.
Abaki ya dun ga bata abincin sai da ta ce ya isheta sannan ya rabu da ita yaci nasa, a ranar ya matsa wa likita ya sallame su, da ya ce ya bari sai gobe ta ƙara samun ƙarfin jikinta yaƙi.
A ranar gidan Hajiya ta kwana a ɗakinta akan gadonta zo ku ga yadda Hajiya ke ji da Sakinaa. Washe gari tun da safe mai lalle tazo ta zanawa Sakinaa uban ubansu haka mai saloon da me kwalliya, bayan ya bushe aka mata wankan dilka zo ku ga kwalliya. Ma sha Allahu ƙyawun Sakinaa ya ƙara fitowa ainun.
Ƙayatacciyar liyafa aka gabatar a wani babban holl, ai susucewa Mubarak ya yi da ya ga Sakinaarsa hannunsu na sakaye da  juna, sai wani irin kallo yake ai ka mata kai daga gani na tsantsar sha'awa da so ne.
Haka aka gabatar da liyafar cikin kwanciyar hankali, kafin a kammala tuni Mubarak ya fara zuzucewa.
Gidan Hajiya aka mayar da ita, Da Hajiyar ta ce ya bari gobe sai a kai ta amma yaƙi, ya ce a kai masa matarsa yau, nan aka fara shirin kai ta domin ita duk abinda Mubarak ya ce shi take yi. Ɗan so kenan.
Ƙawayenta su ne suka kai Sakinaa katafaran gidan Mubarak iya haɗuwa ya haɗu ba ƙarya gida ne na gani a faɗa bayan kowa ya gama wucewa Ango da abokansa suka shugo inda suka dun ga shaƙiyancinsu abin mamaki har da mata ita dai tana cikin mayafi ba ta iya ɗagowa ba balle

ta kallesu sai dai da alama suna da yawa don yadda take jin muryoyinsu da yawa.
Bayan sun gama shaƙiyancinsu suka musu salla sannan suka ajiyewa Sakinaa kuɗin sayen baki ta bawa ƙawayenta.
Mubarak bayan ya musu rakiya ya dawo, zaunawa ya yi bakin gadon ya ce, "Amarya kin sha ƙamshe." Daga cikin mayafinta tayi murmushi.
"Ba za a buɗe mini kyakkyawar fuskar nan na gani ba ko sai na saya ne?"
A hankali ta yaye duka mayafin suka zubawa juna ido.
"Mubarak kafi ƙarfi komai a gare ni, fuskata fuskarka ce bazan taɓa cewa sai ka biya ni kafin ka kalle ni ba, da ni da kai duka abu guda ne." Murmushin jin daɗi ya saki.
"Na gode my Sakinaa ina sonki da yawa."
Numfasawa tayi,
"Nima ina sonka Mubarak burina dai ka riƙe ni amana karka juya mini baya saboda kai nabar ahlina don Allah Mubarak ka riƙe ni amana."
Ta faɗa a raunane tare da haɗe hannayenta waje guda a lamar roƙo, riƙe hannayen nata ya yi yana murzawa a hankali "Sakinaa ni da ke daga yanzun mun zamo abu guda ne ba najin zan iya juya miki baya har abada kisa a ran ki Mubarak yana tare da ke har ƙarshen rayuwarki."
Murmushi tayi cike da jin daɗin furucinsa ta ce, "Na gode Habibi." Shima murmushi ya yi,
"Ki tashi mu gabatar da sallah domin nuna godiyarmu gurin Allah." Babu musu ta tashi toilet ta shiga ta ɗauro alwala, bayan ta fito shima ya shiga.
Sai dai babban tashin hankalin da Sakinaa ta fara riska tattare da Mubarak shi ne rashin iya sallah, sam babu abinda ya sani gami da ibadarsa don ko fatiha da kyar ya kawota. Shuru tayi gabanta na faɗuwa a ran ta kuwa ta sa zata koyar da shi abinda ta sani domin ya gyara ibadarsa, bayan sun idar jikinta a sanyaye tana kallonsa cike da tausayi shi kuwa ko ajikinsa wai an tsikari kakkausa, ledar da suka shugo da ita ya jawo ban ƙararriyar kaza ce da su fresh milk, nan suka ɗanci duk da Sakinaa ta ƙi ci shine ya tilastata sannan ya bata a baki.
Bayan sun gama tana niyyar shiga bathroom ta wanke baki sannan ta watsa ruwa amma ya riƙeta, cikin jin kunya ta ce, "Bari na dan watsa ruwa." Ƙiri-ƙiri ya hanata nan fa labarin ya canza salo.
Sakinaa taci baƙar wuya hannun Mubarak sam bai tausaya mata na ganinta ƙaramar yarinya ba, ya mance ba irin 'yan matansa ba ce da yake harka da su, a gareta wannan ne na farko, saboda azaba sumewa tayi, sai da ya gama hankalin sa ya dawo jikinsa sannan ya ga katoɓarar da ya yi.
Kinkimarta ya yi zuwa bathroom nan ya sakata cikin ruwan zafi, jin ta cikin ruwan zafi ya farfaɗo da ita ta saki kuka, haka dai ya yi ta gasata harta ɗan sami sauki.
Sai sambatu yake mata "Ni daman irin matar da nake so kenan Sakinaa ki ce daidai da ratuwata komai naki yayi mini haka nake so." Ita ko magana ta kasa a ranta kuwa mamakinsa take, tunowa da tayi babu addu'ar da ya yi kuma ya sameta cikakkiyar budurwa maimakon ya godewa Allah sai faman sambatun banza yake da ba su da wani tasiri a gareta.
Haka fa Sakinaa kullum suke cikin amarcinsu, maimakon aga amarya na kyau da ƙiba kamar ko wacce amarya sai aka samu akasin haka wannan karon, domin Sakinaa duhu tayi sosai ga rama saboda tunani, sai dai tayi fresh abin ta domin sam Mubarak ya fara fitar mata a rai saboda zuwa yanzu da suke wata biyu da aure ta gama fahimtar duka halayensa kama daga rashin ilminsa shaye shayensa neman matansa da duk wani abu, duk da zuciyarta nanan

kumshe da son sa bata ganin laifinsa ga yawan takura mata da yake da nema wannan shi ne yafi ɗaga mata hankali don bai mata da sauki.
Wani zuwa da Hajiya tayi taga yadda ta rame ta tambayeta sai ta ce ba komai suna zamansu lafiya.
Watansu huɗu da aure Sakinaa ta fara ciwo yawan amai da rashin cin abinci ko da sukaje asibiti likita yatabbatar musu ta sami ciki na wata biyu.
A furgice Mubarak ya miƙe yana kallon likitan "Doctor ciki fa ka ce wanne irin ciki wata huɗu kachal da aure?" Daga likitan har Sakinaa bin sa su ka yi da kallo cike da mamaki.
Likita ya ce"Wannan ai abin farin ciki ne Allah ya baka sai ka miƙa godiyarka gare shi baka butulce masa ba." Cikin fusata ya ce, "To ban shiryawa zama uba a wannan matakin ba, idan zaka zubar to ka zubar na biyaka idan kuma bazaka iya ba sai muje gurin masu zubar wa."
Likita ya ce, "A'a mu ba mu zubda ciki ka iya tafiya." Fin cikar hannun Sakinaa ya yi su ka yi waje ita kuwa dubansa take cike da tashin hankali, sai da ta zauna cikin mota ta iya kakalo kalamanta domin tuni yawun bakinta suka kame, "Mubarak me nake ji haka? Kana nufin baka son cikin da ke jikina ko ya?"
"Tabbas ban shirya zama uba a yanzu ba, to ke Sakinaa in ban da abin ki mene ne abin ɗaukar ciki a wannan lokacin haka nan kawai ki kashe mana jin daɗinmu ki zo ki tsufar da kan ki, ba ma wannan ba kina ganin dai makaranta ki ke zuwa ko secondary ba ki gama ba, ke wannan ba abin kunya ba ne ƙawayenki su ganki da ciki?"
Kallonsa kawai take don ta kasa maganantuwa juya kalamansa kawai take a ran ta, lallai mutumin nan babban jahili ne, shi yanzu har zai iya cewa sai lokacin da ya yi niyya sannan zai haihu to shi ke da rayuwarsa ma ko kuwa shi ke ba da haihuwar da zai zaɓi lokacin da yake so sannan ya haihu? Hankalinta ya sake tashi lokacin da ta tuno hirar da suka taɓayi da Hamma Umar, inda wata rana suna zaune ya kalle ta ya ce, "Wallahi Sakinaa yara suna burge ni, ina sha'awarar na ga yara suna ta shawaginsu da wasansu cikin gidana." A lokacin ta ce,
"Chaf ka ce zaka tara yara da yawa?"
"In sha Allahu idan Allah ya ba ni zanyi farin ciki ko su nawa ne." Ta saka dariya.
"Lallai Hamma Umar ka ce mata huɗu zaka aje a gidanka?"
Murmushi ya yi tare da furta,
"Sakinaa kenan duk mace guda nake so ta haifa mini yaran nan ni ba ni da sha'awar tara mata fiye da ɗaya."
"Lallai matar nan taka ta shigenge idan ita kaɗai zata haifa maka yara da yawa."
"To mene ne a ciki? Fatana dai Allah ya ba ni masu albarka waɗanda zan yi alfahari da su watan wata rana."
Ta amsa da amin tana ma sa wani irin kallo, lokacin da ya ɗago suka haɗa ido ta sadda kai ƙasa da sauri, matsananciyar kunya ta rufe ta....
08104335144

*Albishir ga masu karanta Littafin WANKA DA GARI mutum 10 ɗin farko da suka fara biya to na musu rangwame akan su turo 400 kamar yadda na ce mutum 10 na farko don haka dama ce ga duk waɗanda zasu fara biya kafin book 1 ya kammala, da zarar na kammala book 1 duk mai buƙatar WANKA DA GARI zai biya kuɗi 700*

_Zaku iya turawa kai tsaye ta wannan account 0037219728 Fatima Rabiu Sunusi StanbicIBTC sai a tura shaidar biya ta wannan number 08104335144_

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUku
#LabarinSakina2024
_Gawurtattu uku 2024_

WANKA DA GARI...

©UmmuAffan

*Book 1 Page 13-14*

Ina kuke mata? Mata nake magana waɗanda suka amsa sunansu na mata ba muna mata ba! Kaya ne masu inganci waɗanda zai mai rabo ke samu. Ki buɗe bakin aljihu Hajiyata kiyi gyara da ingantattun kayanmu na GHT muna da.
Royal jelly-karin Niima jiki yayi kyau yyi sulbi kamar tawarda.
Akwai Garlic oil _maganin infection sadidan ga tightening da yke ka sa skin kyau sa namiji sunbatu.
Muna da Ganoderma reishi _xai ciccciko Miki da gaba ya motso d shaawa ya matse mace gam Yana gigita maxa.
Sannan akwai Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Ba anan muka tsaya ba muna da irin su Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Da su Longzit-matan da suka Kai shekaru 40 Niima y fara karanci a jikin su ku Sha longzit ku bn labari.
Ga Panicept_duk wani ciwon Kashi da gabobi in Sha Allah matsala t kau.
Kuma akwai Sto care_ina masu ulcer duk karfin ulcer in Sha Allah xai magance masu shekara da shekaru Basu Yi axumi b sun gwada sun fara axumi ynxu.
Da Female _masu matsalar alada , infection,rikecewar jini matsi duk wata harka t gaban mace in Sha Allah.
Duk abin da kake buƙata zaka samu daga GHT sayen nagari mai da kuɗi gida kai tsaye kayi wa wannan number mgn domin haɗaku da sha yanzu magani yanzu wato Maman Amal GHT 08104335144

Shahararru goma a duniyar kayan mata Maman Zee ƙamshi and Kayan mata, duk wasu nau'i na kayan mata na gargajiya da na zamani gumba tsumi tabaje zuma masu ƙyau da inganci ku nemi maman zee ƙamshi an kayan mata a number kamar haka 0806 384 5136 Tana Bauchi tana aika kayanta gari-gari Kasa-ƙasa. Sayen na gari mai da kuɗi gida.

*Masu buƙatar ɗaura musu tallah suyi mgn cikin farashi mai sauƙi.* A saman rubutu ko a ƙasa ko wanne da farashinsa. Na gode.

Hawaye ne suka ɓalle mata lokacin da ta kammala tuno wannan zantuka, da haka suka isa wani ƙaramin asibiti, bayan ya yi parking suka fito har zuwa lokacin a fusace yake. Kama hannuwanta ya yi suka shiga ciki.
Wani likita suka gani da wasu 'yan mata biyu, bayan ya sallame su su Sakinaa ma suka shiga, bin bayansu tayi da kallo ganin yadda ɗayar ke ɗin gishi, bayan sun zauna Mubarak ya sanar da shi yana san ya zubda cikin jikin Sakinaa. Kallonta ya yi sosai sannan ya kalli Mubarak.
"Ita ma wannan cikin kayi mata? Amma a fuska kamar yarinyar ƙwarai duk da dai da kama ake ƙota amma ba a gane abin da ke kan fuska, ko dai tilasta mata kayi?"
Gaban Sakinaa ne ya tsananta faɗuwa, ta zubawa Mubarak ido yayin da shima ita ya kalla. A ɗan rikice, sannan ya kalli likitan muryarsa da alamun rashin gaskiya.
"Haba Doctor Mansir mene ne hakan? Amma sa nake na sanar da kai ɗaurin aurena kuma kai ma kaje, ai kuwa labarin zuciya a tambayi fuska ko, sannan zaka kawo mini wata maganar banza?"
Kallon Sakinaa ya sake yi "Ohkey na man ce wannan ita ce matar taka?"
"I," ya amsa masa a takaice. Jinjina kai ya yi sannan amsa.
"M.B ga shawara da zan baka." Da yake haka suke kiransa har abokansa, yaci gaba da cewa
"Wannan matarka ce ta sunna bai kamata ka zubda mata ciki ba." A harzuƙe Mubarak ya taso
"Ka ga malam, ba yau muka saba harkar nan ba zaka zubda ko kuwa muje wani wajen?" Cike da tausayin Sakinaa ya amsa, wacce zuwa lokacin kuka take sosai gashi ta kasa musawa Mubarak duk abinda ya yi ko taji haushi a zuciyarta to bazata iya nuna masa a fili ba.
Haka a ka shigar da ita wani ƙaramin ɗaki ya ciro kayan aikinsa sai lokacin ta sami bakin magana, cikin hawaye ta ce, "Doctor ka tausaya mini don Allah kar ka zubar mini da ciki kamar yadda ya bukata." Kallonta ya yi cike da tausayi tabbas tun farkon shugowarsu yaji tausayinta.
"Kar ki damu ni ma ba ni da niyyar cire miki amma dole na miki wani abun da zai ga kamar na cire miki kema sai ki iya taknki." Numfashi taja tare da masa godiya sosai.
Mubarak ne ya shugo hannunsa rungume a ƙirjinsa yana ƙare musu kallon kafin ya furta,
"Wai Doctor Mansir me ka ke jira ne har yanzu?" Ajiyar zuciya Sakinaa ta saki yayin da kuma Doctor ya ce "Aikin nake yi ka jiramu waje."
Fita ya yi kawai.
Nan ya mata allurar bacci ya ce, "Nan da awa guda zaki farka lokacin sai ki san ƙaryar da zaki

masa ni dai kawai na taimaka miki ne saboda hakanan naji kin ba ni tausayi." Godiya ta masa nan kuwa ba a ɗauki lokaci ba bacci ya kwasheta.
Mubarak ya kallesa "ina ganin dai aiki yayi kyau?" Numfashi Doctor yaja bayan ya sami guri ya zauna, "To muna saran haka amma gaskiya aikiin ya ba ni wahala."
"Kana nufin bai fita ba kenan?"
"No kawai dai ina sa ran ace ya fitan."
Shuru dukansu sukayi na wani lokaci kafin Doctor ya sake cewa, "Na mata allurar bacci ta sami bacci yanzu." Miƙewa Mubarak ya yi tare da jefa masa kuɗi ya nufi ciki kinkimarta ya yi ya fita Doctor ya bi su da kallo.
Bayan mota ya sakata shima ya zagayo ya shiga sannan ya ta da, kai tsaye gida suka wuce. Sai dai Sakinaa farkowa tayi ta ganta a gida, da sauri ta shafa cikinta hawaye masu zafi suka gangaro mata.
Haka rayuwar tacigaba da tafiya inda Sakinaa ke matukar daurewa da nuna masa bata da ciki take komai kamar da sai dai ita kaɗai ta san wahalar da take sha.
Aka ce shi ciki ɗan duma ne ko an ɓoyesa idan lokacin fitowarsa ya yi to zai fito, hakan ta kasance a gidan Sakinaa da Mubarak.
Lokacin da cikin Sakinaa ya shiga wata shidda tuni ya fito saboda ita ɗin mai girman ciki ce, duk da ɓoyen da take da saka manyan kayan da suka mata yawa sai da Mubarak ya gane inda ya ke ce mata "Me nake gani Sakinaa kamar ciki a jikinki?" Dabarcewa tayi ta fara kakkaucewa inda ta ce,
"Haba dai ni kaina kwana biyun nan na ga ina ta tumbi." Cike da rashin yarda ya ce ta sako mayafinta tazo.
Babu musu tasa ta fito don bata daɗe da fitowa wanka ba, mota yaja su ita dai ƙirjinta tara-tara kawai yake bugu, da haka har suka kai asibiti, gwajen farko ya nuna ciki ne da ita har wata shidda, nan fa Mubarak ya dunga masifa wai a zubda, hawaye ne ya gangaro a fuskar Sakinaa ta ce, "Bazai yuwu ba!" Ta furta da ƙarfi.
Kallonta ya yi cike da mamaki, "Me ki ke nufi?" "abinda kunnuwanka ya jiye maka, Mubarak ina so ka sani bazan yarda ka zubda mini ciki a wannan karon ba, duk da daman shine babu inda yaje."
Sosai yake dubanta ganin yadda take masa masifa, matsowa ya yi kusa da ita sosai. "Sakinaa ni ki ke faɗawa ba za a fitar da cikin ba?" Gyaɗa masa kai tayi cike da rashin tsoro,
"Ƙwarai kuwa Mubarak ina so ka sani sai dai ka kashe ni akan cikin nan domin bazan yarda ba."
Ɗaga hannu ya yi ya zuba mata wani lafiyayyen mari, da sauri ta riƙe kuncin tana kuka, likitan ne ya ce, "Haba bawan Allah mene ne haka ne? Tunda ta ce bata so ka bar mata a bin ta mana, ba sai kabarta ba." Duk a tunanin likitan ko budurwarsa ce ya yi wa ciki.
Juyawa Sakinaa tayi ta fice daga office ɗin shima yabi bayanta, kai tsaye ficewa tayi daga asibitin tana kuka sosai. Mota ya shiga yabi bayanta gabanta ya yi parking.
"Shugo ciki." Banza ta masa zata juya, ya daka mata tsawa ba don taso ba ta shiga motar ya fuzgeta sai gidan Hajiyarsa.
Suna isa ya yi parking, fitarsa ya yi ransa a matukar harziƙe. Tana hawaye tabi bayansa, ko sallama babu ya shiga kai tsaye.
A ruɗe Hajiyar take kallonsa kafin ta iya furta, "My son lafiya kuwa?" Zaunawa ya yi daidai shugowar Sakinaa ya ce, "Daga asibiti muke wai ciki ne da ita suka ce." Nan take Fuskar Hajiya

ta cika da annuri ta washe baki.
"Kai Alhamdulillah amma nayi farinciki aure ya yi albarka nima na kusan zama kaka zan sami jika."
A ƙufule ya kalleta. "Haba Hajiya nifa cikin nan ba wai ina maraba da shi ba ne nazo ne don kisan hanyar da za a bi a cire mata shi."
Numfashi taja, "Haba Mubarak kyauta ce fa Allah ya baka don Allah kabar wannan maganar, ko ɗaya ne ai ka bari ta aifa kafin ku fara tsarin iyali."
Ta janyo Sakinaa kusa da ita tana mata sannu tare da bata haƙuri.
Iya ƙuluwa ya ƙulu, miƙewa ya yi ransa a ɓace ya ce, "Tunda haka ki ka ce to na bar miki ita idan ta haihu ta yaye abin ta bar miki sai ta dawo." Ya fita a fusace, kuka Sakinaa ta fashe da shi yayin da Hajiya da Laurah suke ba ta baki akan tayi haƙuri.
Gaskiya ba laifi sosai Hajiya da ƙannan Mubarak ke kula da Sakinaa tabbas suna ba ta kulawa don suna son cikin sosai, kome ta keso shi suke mata kuma cikin so da jin daɗi. Tun daga ranar da Mubarak ya tafi ba ta sake ganinsa a gidan ba har zuwa lokacin da ta haifi kyakkyawar yarinyarta a asibiti mai kama da Sakinaa sak. Tabbas Hajiya da sauran dangin Mubarak sunyi murna.
Bayan mun koma gida aka kira Mubarak aka sanar masa na haihu babu abinda ya ce saidai ya turo makudan kuɗaɗe akan ayi duk abinda ya dace, sosai Sakinaa tayi kuka a ranar, iyayenta suka faɗo mata, bata taɓa kewarsu irin ta ranar ba.
Bata san dalili ba amma tunda tayi aure ba ta taɓa tunosu ba sai ranar, sannan kuma sam na mance da su. Yanzun ma da ta tunosu gabanta ne ke wani mugun zafi da turiri nan take kuwa ciwon kai mai tsananin zafi ya rufe ta.
Zaliha ce ta faɗo mata a zuciya, tun bayan lokacin da suka zana waec da neco rabonta da ita, wayarta ta ciro ta danna lambarta ringing biyu ta ɗauka, dukansu shuru ya biyo baya, zuwa cen Sakinaa ta daure ta maganantu "Assalamu alaiki!" Amsawa tayi Suka sake shuru. Can dai ta ce, "Sakinaa manya yau an tuno mu ne?" Hawayen da suka gangaro mata ta goge sannan cikin sassauta murya ta ce, "Zaliha daman na haihu ne jiya."
Cike da murna ta ce, "Kai barka Sakinaa na tayaki murna Allah ya raya me aka samu?"
"Mace.!"
"To Allah ya raya sai nazo." Sallama muka yi nayi zugun da waya a hannuna tabbas yadda Zaliha ta amshe ni a waya ban taɓa zato ba. Na ɗauka ma ko wayata ba zata ɗauka ba sai ta shayar da ni mamaki.
Ɓangaran Zaliha kuwa, wayar tabi da kallo jikinta a sanyaye ta furta, "Tabbas rabo shi ne ya kai Sakinaa gidan Mubarak balle rabon 'ya mace shi mai zafi ne, wani kuma baya taɓa aihuwar ɗan wani."
Daman shiri take domin a ranar ne bikin Hamma Umar da Zubaidaa. Bayan tayi wa mahaifiyarta sallama ta wuce gidansu Sakinaa domin tare za su tafi da Umma.
Bayan sun gaisa take sanar mata Sakinaa ta haihu, ƙura mata ido tayi "A ina ki ka ji Zaliha?"
"Ita ta ce da kan ta ta kira ni." Numfashi Umma taja tare da cewa Allah ya raya, Sannan suka wuce gidan bikin.
Tabbas anyi biki na yaran gata an kashe kuɗi sannan anci ansha zo kuga Hamma Umar Faruuƙ saboda tsabar kyau kamar ka sace sa ka gudu, ya yi kyau abin ku ga masu kyan, ita kanta Zubaidaa babu laifi tayi kyau sosai.

Ba zaka taɓa gane yanayin halin da Hamma Umar yake ciki ba, kawai dai shi daman haka yake cikin farin ciki ko a kasin hakan ba cika ganewa ake a fuskarsa ba sai dai fuskar nan tasa na cike da kwarjini da annuri.
Bayan kammala biki su Zaliha suka koma gida sai fatan Allah ya ba wa amarya da ango zaman lafiya.
A ranar da safe Sakinaa ce zaune ita da Larah suna hira su kaji an saka guda ana sanarwar auren Umar Alkasim Inuwa da Zubaidaat Bello Inuwa, A tv ƙirjin Sakinaa ne ya buga da karfi, sake ƙwalalo ido tayi tana kallon photonsa da amaryarsa yadda suka yi wani fitinannan kyau.
Larah ta ce "Allah sarki Umar gayen nan ya yi wallahi tare muke karatu da shi amma shi yanzu har ya yi mester kin san dan jarida ne ance yana aiki gidan redion taraiya na Kaduna wallahi ina mugun son gayen nan, shiyasa na sayi redio saboda shi kawai nike jin shirye-shiryensa musamman news da yake na turanci karfe 2 na rana uhmmm wallahi idan kina saurara har wani lumshe ido zaki dunga yi saboda daɗin muryarsa ga iya turanci kamar baƙin bature.
Jiki a sanyaye Sakinaa ta kalleta, "Daman ya gama karatu ne?"
"To har ya fara aiki wannan gayen da ki ke gani ƙwararre ne a fagen aikisa ɗan jarida ne jajirtacce kuma na gari wallahi naso gayen nan ga shi ya yi aure abin shi."
Shuru tayi inda Larah taci gaba da yabon Umar in ban da ligude babu abinda zuciyar Sakinaa ke yi.
Zaliha tazo sosai Sakinaa ta cika da mamaki, inda take tambayarta daman tasan gidan? I kawai ta amsa mat a takaice ganin kamar bata son mata maganar ta rabu da ita, don neman shiri take ita kawaice zata iya kalla tamkar kalla 'yar'uwarta.
Haka ta jera kullum sai tazo har akayi suna abin ya yi wa Sakinaa daɗi domin ranar sunan har da ƙawayensu na makaranta duk ta gayyato wanda su kai aure da 'yan mata.
Yarinya ta amsa sunan Hajiya wato Rumasa'u sai ake kiranta da Yusra.
Washe garin suna da wuri Zaliha tazo da ita a kayi komai na suya, domin ƙaton Sa da raguna biyu da Hajiyar ta yanka a sunan Yusra.
Ba laifi Hajiyar ta yi wa Sakinaa kaya haka danginsu da ƙawayenta sosai suka yi mana ƙyautar kaya suma ƙawayensu Sakinaa da suka zo ba laifi sun yi nasu haka Zaliha ta mata abin arziƙi, da zata tafi ita ma ta haɗata mata sha tara ta arziƙi, kin amsa tayi sai da na haɗata da Hajiya sannan ta amsa muka yi sallama.
Haka Sakinaa taci gaba da renon 'yar ta cike da kulawar Hajiya har suka shekara guda, babu Mubarak ba ɗuriyarsa zuwa lokacin tuni Yusra tayi wayau har tafiya ta iya don yarunya ce mai kazar-kazar ga wayau.
Kwatsam wata rana suna zaune a parlour suna kallo sai ga sallamar Mubarak abin ya ba su mamaki duka suka bi shi da kallo zuba wa Sakinaa ido ya yi yana kallonta kai tsaye kuwa gurinta ya nufo ko kunyar su Hajiya bai ji ba ya wani zauna kusa da ita sosai yana aika mata wani kallo ƙasa-ƙasa....

*Albishir ga masu karanta Littafin WANKA DA GARI mutum 10 ɗin farko da suka fara biya to na musu rangwame akan su turo 400 kamar yadda na ce mutum 10 na farko don haka dama ce ga duk waɗanda zasu fara biya kafin book 1 ya kammala, da zarar na kammala book 1 duk mai buƙatar WANKA DA GARI zai biya kuɗi 700*

_Zaku iya turawa kai tsaye ta wannan account 0037219728 Fatima Rabiu Sunusi StanbicIBTC_
Shaidar biya ta wannan lamba 08104335144

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUku
#LabarinSakina2024
_Gawurtattu uku 2024_

WANKA DA GARI...

©UmmuAffan

*Book 1 Page 15-16*

Ina kuke mata? Mata nake magana waɗanda suka amsa sunansu na mata ba muna mata ba!
Kaya ne masu inganci waɗanda zai mai rabo ke samu. Ki buɗe bakin aljihu Hajiyata kiyi gyara da ingantattun kayanmu na GHT muna da.
Royal jelly-karin Niima jiki yayi kyau yyi sulbi kamar tawarda.
Akwai Garlic oil _maganin infection sadidan ga tightening da yke ka sa skin kyau sa namiji sunbatu.
Muna da Ganoderma reishi _xai ciccciko Miki da gaba ya motso d shaawa ya matse mace gam Yana gigita maxa.
Sannan akwai Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Ba anan muka tsaya ba muna da irin su Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Da su Longzit-matan da suka Kai shekaru 40 Niima y fara karanci a jikin su ku Sha longzit ku bn labari.
Ga Panicept_duk wani ciwon Kashi da gabobi in Sha Allah matsala t kau.
Kuma akwai Sto care_ina masu ulcer duk karfin ulcer in Sha Allah xai magance masu shekara da shekaru Basu Yi axumi b sun gwada sun fara axumi ynxu.
Da Female _masu matsalar alada , infection,rikecewar jini matsi duk wata harka t gaban mace in Sha Allah.
Duk abin da kake buƙata zaka samu daga GHT sayen nagari mai da kuɗi gida kai tsaye kayi wa wannan number mgn domin haɗaku da sha yanzu magani yanzu wato Maman Amal GHT

08104335144

Shahararru goma a duniyar kayan mata Maman Zee ƙamshi and Kayan mata, duk wasu nau'i na kayan mata na gargajiya da na zamani gumba tsumi tabaje zuma masu ƙyau da inganci ku nemi maman zee ƙamshi an kayan mata a number kamar haka 0806 384 5136 Tana Bauchi tana aika kayanta gari-gari Ƙasa-ƙasa. Sayen na gari mai da kuɗi gida.

*Masu buƙatar ɗaura musu tallah suyi mgn cikin farashi mai sauƙi.* A saman rubutu ko a ƙasa ko wanne da farashinsa. Na gode.

Cike da fushi ta tashi ta nufi bedroom, miƙewa ya yi ya biyota yana kiran sunanta, "Sakinaa! Keenahta! Haba Keenar Mubarak.
Tana shiga ta faɗa saman gadonta tana kuka, shugowa ya yi ya zauna bakin gadon tare da riƙo hannayenta da sauri ta fizge cikin kuka ta ce, "Me zaka ce mini? Mubarak me zaka ce mini? Bayan ka gama cutar da rayuwata ka cutar da ni!" Rufe mata baki ya yi alamar tayi shuru, ya fara girgixa mata kai.
"Ba zaki ga ne ba Sakinaa."
"Taya kuwa zan ga ne tunda ka cutar da..."
Jawo ta ya yi jikinsa cikin sigar rarrashi ya furta, "Kiyi shuru Sakinaata kar aji mu, don Allah kiyi haƙuri ki yafe mini na gane kuskurena nasan ban ƙyauta miki ba daga ke har 'yar mu, na dawo ne domin gane kurena domin na gano wanka da gari ba shi maganin yunwa sai an jiƙa kafin asha."
Da sauri ta kalle shi.
"Iye! Yau kaine ke kiran Yusra 'ya bayan ka ce baka sonta?"
"Haba dai baby taya zan ce ba na son 'yata, bayan nasan jinina ce. Wallahi kin ji na rantse ina kaunar 'yata kuma ta nan matsayinta na 'yata."
Ajiyar zuciya ta saki, taji ranta ya mata sanyi, domin ta shiga furgicin jin ya sadaukar mata da 'yarsu, amma yanzu ranta wasai. Nan ya dinga zuba mata roman baka da daɗaɗan kalamai tuni Sakinaa ta yarda da maganarsa har taji ranta ya mata sanyi.
Kunsan mace da rauni daman tsakanin mata da miji kuma sai Allah.
Sai kawai gani a ka yi sun fito suna dariya, ko daman Hajiya tasan za a rina, wai an saci zanin mahaukaciya domin tasan da hakan zai iya faruwa don tuni ta ƙara dantse kamo na tsakanin Mubarak da Sakinaa duk abinda Mubarak ke so to ita ma shi take so sannan zata iyayin komai akan farin cikin ɗanta mafi soyuwa a zuciyarta.
A ranar suka tattara sai gidansu, sai dai sun bar wa Hajiya Yusra da sunan Muhsin ƙanin Mubarak zai kawota da dare, nan kuwa tuni sun gama magana kan zata zauna ne an yayeta amma Sakinaa bata san komai ba akan hakan.
Gidan tsaf suka iske shi tunda daman Mubarak a nan yake kwana, kuma 'yan matasansa duka suna zuwa, amma daga ranar ya taka musu burkin kar wacce ta sake zuwa matar gidan zata

dawo.
Tunda suka dawo sai aka lula duniyar soyayya ta ma'aurata, daman ya musu take-away ba wani girki za ta yi ba, ganin har taran dare ba kawo Yusra ba ta ce,
"Wai ni Abban Yusra ya naji Yusra shuru ne?"
Ya mutsa fuska ya yi "Ku kenan matan hausawa da an haifi yaro ko yarinya shi kenan miji ya koma baban wance ko Daddyn wance ko Abban wance haba ba za ku faɗi suna mai daɗi ba?"
Murmushi ta yi "Sorry Abban Yusr... Ayya sorry my honey." Taɓe baki ya yi "Kin kai su dai idan kaya ne."
"Wa wannan ba naji Yusra shuru?"
"Kiyi haƙuri My Sakinaa nasa Hajiya ta yayeta ne." Zaro idanuwa tayi.
"Yaye kuma Abban Yusra shekararta guda fa kenan?"
"I ai Hajiya ta ce ana yaye har 'yan shekara daya."
Tagumi ta saka tare da zuba masa ido zuciyarta na faɗa mata anya Mubarak ba sha'awarta kawai yake ba, ta lura kawai shi ita ya sani alamunsa suna nuna hakan, amma wani ɓangare na zuciyarta ya kasa gasgata hakan, haka tayi haƙuri aka yaye Yusra wacce ke da shekara guda kachal.
Ana wata ga wata, ai dawowarsu da wata guda sai ga wani cikin a jikin Sakinaa, zo kuka durama tatur Mubarak ya nuna sai dai a zubda cikin wannan karon ma taƙi yarda, zuciyarta ba ta taɓa dakewa irin ta wannan karon ba, abu ya sake kai su gaban Hajiya wannan karon ma bayan Sakinaa tabi domin ita mace ce mai son yara, musamman ma da suka fito daga ɗan lelanta, nan fa Mubarak ya dunga masifa da zage-zage "Mace sai ka ce tunkiya ko kaza da antaɓa sai ciki shi wallahi ba haihuwa ya aurota ta dunga masa ba.
Zai fita Sakinaa ta bi shi ya ce, "Ina zaki bi ni kamar raƙumi da akala?"
"Gidan mijina mana!" Mtsuuw! Ya ja tsaki mai ƙara. "Ai yanzun ma sai dai ki zauna anan idan kin haihu kin yaye sai ki koma." Harara ta banka ma shi.
"Bari kaji Mubarak wallahi baka isa ba, ƙafarka ƙafata ba inda zan zauna sai gidanka." Harara ya banka mata itama ta mayar masa ficewa ya yi ta bi sa, ko a mota ba wanda ya yi wa wani magana har suka isa gida.
Tunda suka dawo sai Mubarak ya haɗa kayansa cikin ƙaramar akwati ya bar mata gidan "Wallahi bazan zauna ina ganin bakin ciki ba, gara ni nabar miki gidan." "Au yaji zaka yi, yau na shiga uku ni Sakinaa namiji da yin da daka barkono ya bar gidansa." Ko kulata bai yi ba, bayan fitarsa ta zauna ta saki kuka wannan wacce irin rayuwa ce haka.
Tun tana jin tsoron kwana ita ɗaya a gidan har ta saba, haka ta reni cikinta har zuwa lokacin haihuwa, da kanta taje asibitin da take awo, da taji alamar haihuwa cikin ikon Allah ta haifi ɗanta lafiya, sai bayan ta koma gida sannan ta kira Hajiya ta sanar mata, aikuwa sai gata da ƙannan Mubarak sun zo.
Wannan karon ma anyi abin arziƙi sosai yaro ya amsa sunan mahaifin Sakinaa, domin Hajiya tambayarta tayi sunan da take so sai ta ce ABDULLAHI sai ake kiransa Fahat wannan karon ma Zaliha tazo kuma tayo gaiyatar ƙawayensu kamar wancen, anyi komai cikin girma.
Haka take rainon yaranta biyu, don Yusra ma ta dawo gabanta, sai da ta yaye Fahat sannan Mubarak ya dawo gidan, wannab karon ma zuba mata daɗaɗan kalamai ya yi harta aminta da shi, inda ita roman bake ke mata sauƙin karɓa, ai kuwa suka ci gaba da zamansu na so, da ƙauna Yusra shekararta uku Fahat shekara biyu haka yasa su makarantar renon yara boko da

islamiyya idan suka tafi tun safe sai shidda na yamma suke dawowa gida. Wannan shi ne tushen labarin Sakinaa har zuwa bayan auren Zaliha da Abban Yusra ya yi zuwa sakinta da Hajiya tasa ya yi da kuma Zuwa gidan iyayenta da tayi basa nan, zuwa zamanta saman dandamali tana tuna tushenta.

CIGABAN LABARIN

Sosai Sakinaa ke kuka tare da danasanin abinda ta aikata a rayuwarta, tambayar kanta take to me yasa ma tayi hakan? Iyayenta abin sonta me yasa zata gujesu? Masoyin gaskiya Hamma Umar shi ne ya faɗo mata a rai, wani irin son sa ne ke kwarara a cikin zuciyarta. Allah sarki Hamma Umar wallahi ita ma tana ƙaunarsa ba ta san ya a ka yi ba har ta aikata hakan a gare shi, ta fashe da wani rikitaccen kuka.

Lokaci ɗaya kuma kukan ya tsaya chekk da ta tuno wani abu, Hamma Umar yana aiki gidan redion taraiya, kuma tasan gidan redion da sauri ta miƙe jin ana kwala kiran magrib, titi ta nufa ta sami keke napep ta sanar masa inda zata ta shiga, sai da ta shiga kuma tafara wasiwasin ko shiɗin ya san inda su Abbanta suke, tasan ba zai wuce ya sani ba da haka suka isa gidan redio ta sallami mai adaidata sannan ta nufi gate ɗin.

Kallon sama da kasa mai gadin ya mata, kafin ya ce "Lafiya?"

"Ummm! Ummm daman nazo gurin Hamma Umar ne."

"Wane ne hakan?" Ya tambayeta, shuru tayi zuwa can ta ce, "A ciki yake aiki."

"Cikakken sunansa fa?" Shuru tayi tana tunani kafin ta ce, "UMAR ALKASIM INUWA." Kallonta ya yi cike da rashin yarda ya ce, "Shi ɗin ne Yayanki yaro dan gata dan ƙwalisa wanda ko wacce mace ke rubibi, ko dai kin zo ne domin ki gansa? Ko kina ɗaya daga cikin 'yan matan da ke zuwa takanas su ce suna sonsa?" Gabanta ya buga da ƙarfi 'yan mata kuma har 'yan mata ke zuwa cewa suna son sa, hawaye ya zubo mata. "Idan baza ka bar ni na shiga ba don Allah ka mini magana da shi." Cewa ya yi a'a 'yan mata shugo sai ki zauna zaman jiransa domin bai daɗ da shiga ba zai yi news na 7:00pm da sauri na shiga, na zauna kan bencin Mau gadin ina kara hangen cikin harabar gidan redion.

Hajiya ta kalli Mubarak ta ce, "Wai kai lafiyarka ƙaau kuwa, tun bayan fitar Sakinaa sai safa da marwa ka ke yi wa mutane?" Kallonta ya yi ransa ɓace.

"Wai Hajiya kin kwance Tsafi da sihirin da kika wa Sakinaa ne?"

Numfashi taja "I, amma tun kafin ma na kwance naga da kansa ya rage aiki kasan daman sihiri ba lallai ba ne ya ɗaure a jikin wanda aka yi wa."

Tsaki yaja, "Amma Hajiya kin san dai ina son ta ko mai zai sa ma mu haɗa bakin na saketa? Ni wallahi abin ya fara damuna kin san wace ce Sakinaa kuwa? Ita ɗin ta daban ce ko a cikin mata 'yar baiwa kenan."

Harararsa tayi, "Amma ai kai ka ce kana son sakinta ko shi ya sa ni kuma na ce ka saketa."

Zaliha da ke jin su miƙewa tayi, tare da kallonsu kafin ta ce, "Mubarak zo mu shiga ciki ke kuma Hajiya ki gaida gida."

Zaro ido Hajiyar tayi "Ina magana da ɗana zaki ce haka?" Murmushi Zaliha tayi ta kalli Hajiya sama da ƙasa.

"Hajiya kenan kar ki man ce wani abu guda ni Zaliha ƙawar Sakinaa ce, duk abinda kika ga inayi wallahi saboda ita ne, kin man ce a gabana kika yiwa Sakinaa sihiri bayan kin ci mutumcin iyayenta ita kaɗai suka haifa amma ki ka raba su da 'yarsu akan wani banzan ƙudiri naki, wai

duk abinda ɗanki yake so sai kin masa ke farin cikinsa kike so to ki sa a ranki da zuciyarki daga yanzu zaki fara ɗanɗanar baƙin ciki, wallahi sai na ramawa Sakinaa da iyayenta da masoyinta abinda kuka mata."
Zaro idanuwa Hajiya tayi cike da mamaki, domin daman tuni Mubarak ya shige ciki. Zaliha taci gaba dace wa, "Tabbas ina son ɗanki Mubarak kuma babu wani sihiri da na masa ko nake niyyar masa a'a indai kissa da kisisina na aiki to daga yau zaki fara ɗaukar hukunci, tsohuwar banza mai matacciyar zuciya kawai."
Ai saboda al'ajabi Hajiya kasa maganantuwa tayi har sadda Zaliha ta bar parlourn tabi bayan Mubarak, kafin ta miƙe ta fita da sauri domin a yau take son tayi wa Zaliha hukunci tayi alƙawari a ran ta yau sai ta kashe Zaliha in dai Tsafi na aiki a yau zata rabata da ɗanta, sai dai a ka ce kana naka shi kuma Allah yana nasa, saboda sauri da Hajiya keyi taje ta ida nufinta akan Zaliha idanuwanta duka sun rufe burinta ta isa gida ta hada mummunar nufinta, sakamakon gudun ganganci da take ko gabanta bata kallo sosai ta haɗu da mummunan haɗari a hanyarta ta zuwa gida.
Wa'iyazu billah, mummunan haɗari kuwa domin da ƙyar aka kwakulo Hajiya daga cikin motarta duk ta dagargaje aka nufi asibiti da ita, tunani ake ta mutu ko kuwa da sauran numfashinta, Allah ma sani.
Wajen takwas na dare Umar ya fito daga cikin studio na redion, zuwa lokacin Sakinaa ta sami buta gurin Maigadi duk tayi sallolin dake kanta zaune take tana jiran fitowarsa, yana fitowa Maigadi ya nuna mata shi, da sauri ta miƙe ta nufi gurinsa, yana ƙoƙarin shiga motarsa.
"Hamma Umar!" Ta faɗa a matukar rauna ne, shi kuwa jin muryar da ba zai iya mantawa ba a rayuwarsa yasa shi waigowa da sauri, nan take suka haɗa idanuwansu cikin na juna, zubawa juna ido sukayi, kafin ya yi saurin kauda idanuwansa gareta, yana wani ciccisgewa da basarwa. Sosai take kuka ganin yadda Hamma Umar ya sake haɗuwa kamar bashi ba, kwarjini kamala dattakonsa duk sunan tare da shi, kuka ta fashe masa ta ƙaraso garesa ta duƙa har ƙasa cikin kuka da raunin murya ta ce, "Hamma Umar ka tausaya mini ka haɗani da iyayena idan kasan inda suke naje gida ban same su ba.
Numfashi yaja tare da tamke fuska "Ummm bari na miki kwatan ce." Da sauri ta ɗago idanuwanta da ke cike da hawaye, "Ka kaini mana don Allah.''
"Bazan iya ba." Ya faɗa a takaice, kafin ya yi mata kwatance yadda zata gane sannan ya shiga motarsa ya tadata da gudu ya bar gurin a sittin.
Kuka sosai Sakinaa tasa ka tabi bayan motar da kallo kafin ta tashi ta kakkaɓe jikinta ta koma gurin Maigadi ta amshi kayanta tare da masa alkhairi da godiya ta fita ta sami adaidata sahu ta shiga har zuwa lokacin kuka take kamar ranta zai fita, shi kenan yanzu Hamma Umar ya tsaneta ya za tayi da rayuwarta.....

_WASA FARIN GIRKI, BA A FARA BUGA ƘWALLON BA FA HAR YANZU, SOMIN TAƁI KUKE JI A LABARIN RAYUWAR SAKINAA._

*Albishir ga masu karanta Littafin WANKA DA GARI mutum 20 ɗin farko da suka fara biya to na musu rangwame akan su turo 400 kamar yadda na ce mutum 20 na farko don haka dama ce ga duk waɗanda zasu fara biya kafin book 1 ya kammala, da zarar na kammala book 1 duk mai

buƙatar WANKA DA GARI zai biya kuɗi 700*

_Zaku iya turawa kai tsaye ta wannan account 0037219728 Fatima Rabiu Sunusi StanbicIBTC_
Shaidar biya ta wannan number 08104335144

Mutanenmu na ƙasar Niger zasu turo da 500f na katin Moov ko Orange ta wannan layin 08104335144 idan kuma na kammala book 1 zaku turo 700f ne, Na gode.

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUku
#LabarinSakina2024
_Gawurtattu uku 2024_

WANKA DA GARI...

©UmmuAffan

*Book 1 Page 17-18*

Ina kuke mata? Mata nake magana waɗanda suka amsa sunansu na mata ba muna mata ba! Kaya ne masu inganci waɗanda zai mai rabo ke samu. Ki buɗe bakin aljihu Hajiyata kiyi gyara da ingantattun kayanmu na GHT muna da.
Royal jelly-karin Niima jiki yayi kyau yyi sulbi kamar tawarda.
Akwai Garlic oil _maganin infection sadidan ga tightening da yke ka sa skin kyau sa namiji sunbatu.
Muna da Ganoderma reishi _xai ciccciko Miki da gaba ya motso d shaawa ya matse mace gam Yana gigita maxa.
Sannan akwai Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Ba anan muka tsaya ba muna da irin su Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Da su Longzit-matan da suka Kai shekaru 40 Niima y fara karanci a jikin su ku Sha longzit ku bn labari.
Ga Panicept_duk wani ciwon Kashi da gabobi in Sha Allah matsala t kau.
Kuma akwai Sto care_ina masu ulcer duk karfin ulcer in Sha Allah xai magance masu shekara

da shekaru Basu Yi axumi b sun gwada sun fara axumi ynxu.
Da Female _masu matsalar alada , infection,rikecewar jini matsi duk wata harka t gaban mace in Sha Allah.
Duk abin da kake buƙata zaka samu daga GHT sayen nagari mai da kuɗi gida kai tsaye kayi wa wannan number mgn domin haɗaku da sha yanzu magani yanzu wato Maman Amal GHT 08104335144

Shahararru goma a duniyar kayan mata Maman Zee ƙamshi and Kayan mata, duk wasu nau'i na kayan mata na gargajiya da na zamani gumba tsumi tabaje zuma masu ƙyau da inganci ku nemi maman zee ƙamshi an kayan mata a number kamar haka 0806 384 5136 Tana Bauchi tana aika kayanta gari-gari Ƙasa-ƙasa. Sayen na gari mai da kuɗi gida.

*Masu buƙatar ɗaura musu tallah suyi mgn cikin farashi mai sauƙi.* A saman rubutu ko a ƙasa ko wanne da farashinsa. Na gode.

A haka har suka isa unguwar ta Ɗan mani, saitin gurin da ya ce ta sauka ta ce mai Adaidaita sahun ya tsaya, sannan ta fara kallon layin. Ɓangaren da taje unguwa ce ta masu hali da rufin asiri babu hayaniya sosai, kollon layin kawai take, da kin sauka saitin layin gida na uku mai koren gate. Maganarsa ta ƙarshe a masarrafar sautinta, jan akwatinta tayi ta nufi gidan da take ƙyautata zaton shi ne.
Tsaye tayi bakin gate tana ƙarewa gidan kallo, zuciyarta na aiyana mata anya gidan ne? Gida ne mai ƙyau sosai duk da bai cika girma ba amma ya tsaru, ita da tasan mahaifinta ba mai hali ba ne taya zai gina irin wannan gidan?
Numfashi taja tare da buga gate ɗin gidan, mai gadi ya leƙo, gaishe shi tayi,
"Don Allah gidan Malam Abdullahi bakanike nake nema." Shuru ya yi yana tunani sai ya ce,
"Nan gidan Alhaji Abdullahi ne, ban sani ba koshi ki ke nema."
"Nan dai ne aka ce mini in zo."
"To shugo ki tsaya nayi miki iso ko."
Babu musu ta shugo ta tsaya daga bakin gate ta ciki, shi kuma ya shiga cikin gidan.
Mintoci kaɗan ya dawo ya ce,
"Baiwar Allah ki shiga ya ce shi ne."
Hamdala tayi a fili ta fara taka ƙafarta zuwa ciki har zuwa lokacin ba ta daina mamakin yaushe mahaifinta ya yi kuɗin gina gida haka har da mai gadi ba.
A hankali tayi sallama cikin madaidaicin parlourn wanda ya tsaru sosai da kujeru na alfarma da ƙayataccen tv ta bango, harda ƙaramin dinning table, kai duk dai kayan more rayuwa na zamani an tsara su daidai girman parlourn waɗanda suka dace da shi da kuma tsari.
Daga Abba har Umma zuba mata ido suka yi suna kallonta fuskokinsu ɗauke da mamaki, ita ma su take kallo nan take kuma ta saki wani rikitaccen kuka tayo kansu da gudu bayan ta saki akwatinta, jikin Abba ta faɗa tana wani rikitaccen kuka faɗi take, "Abba da Umma na tuba ku

yafe mini ko na sami sassauci ku taimaka ku yafe mini laifina ko zuciyata zata daidaita ina cikin wani hali, nayi nadama wallahi Abbana na gane kuskurena."
Kuka take tamkar zata ƙarar da hawayen idaniyarta, Dukansu kallonta suke, a ka ce tsakanin 'ya da mahaifi ko mahaifiya sai Allah musamman uwa, nan take zuciyoyinsu su kayi sanyi musamman da suka tuno ba laifinta ba ne, domin tun lokacin da Abba yayi istihara ya gane wani babban ƙulli aka kullawa Sakinaa tun daga lokacin suke cikin addu'a Allah ya kwanceshi, to Alhamdulillah komai yazo ƙarshe tsakaninsu ta dawo hayyacinta harta nemesu, ai kuwa dole su godewa Allah gagara misali mabuwayi, hannu dukansu suka ɗaga sama suna godewa Allah. A nan take ba su labarin zamanta da Mubarak da abinda ya faru a tsakaninsu da zamanta da Hajiya duka bata ɓoye musu ba. Umma har da hawaye saboda kuka ta ce, "Sakinaa ƙaddararki kenan daman Allah ya rubuta hakan ga kuma rabon yara a tsakaninku mun godewa Allah ma da ta hanyar aure aka same su bata hanyar banza ba." Abba ya ce, "Wannan gaskiya ne, ita kuma Hajiya Allah ya shiryeta idan mai shiryuwar ce idan kuma ba mai shiryuwa ba ce Allah ya mana maganinta." Duka suka amsa da amin.
Abba ya ce, "Sakinaa mun yafe miki Allah ya yafe mu baki ɗaya." Rungumesa ta sake yi Umma ta ce, "Allah mun gode maka da ka ceto mana 'ya daga cikin wancen mayuwacin hali." Nan sukayi ta addu'a daga bi sani aka ɓige da hirar yaushe gamo.
Abba ya ce taje tayi wanka taci abinci tayi sallah ta kwanta tayi bacci tunda dare ya yi gobe sai su ɗaura, ba don ta so ba ta miƙe don ta lafe jikin Ummanta. Ɗaki guda suka bata daman 3 bedrooms ne sai parlour da kitchen, sannan a ko wanne ɗaki akwai toilet.
Faɗawa tayi saman katifar dake dakin tana jin sabon wani farin ciki na baibayeta, iyaye babu abinda ya kai su daɗi tabbas wanda ya ra sa su dole ya yi kuka. (Allah ya ƙarawa iyayenmu lafiya da nisan kwana, waɗanda kuma suka rasa iyaye Allah yaji ƙansu amin).
Miƙewa tayi ta faɗa toilet wanka tayi tare da ɗauro alwala, bayan ta fito ta ga Umma ta shugo mata da abinci da sauri ta amsheta tana mata sannu.
"Umma da ma kin bari da nayi sallah zan je kitchen ɗin na ɗauka."
"Kar ki damu kici ki samu ki kwanta ki huta." Murmushin jin daɗi tayi tare da furta.
"Na gode sosai Ummata."
Bayan fitar Umma ta buɗe akwatinta ta ciri rigar bacci da zani da hijab, bayan ta idar da sallar isha'i da shafa'i da wuturi, ta cire zanin da hijab taci abincin Ummanta mai ɗan karen daɗi wanda tayi missing shekaru kusan hudu kenan.
Washe gari tun asuba Sakinaa ta tashi ta gyara gidan fes, sannan tayi abin karyawa ta jera bisa dinning. Abba da ya dawo masallaci ya ga tana jera kuloli ga gidan sai ƙamshin turaren wuta yake ya ce, "Sakinaa daga zuwa sai fara aiki ba zaki bari ki huta ba?" Duƙawa tayi har kasa ta gaishe shi ya amsa cikin fara'a, ita ma dariya tayi ta ce, "Haba Abba ai babu batun baƙunta." Dariya ya yi tare da shafa kanta ya ce "Allah ya miki albarka." Ta amsa da amin tana jin farin ciki wanda rabon da taji shi tun zamanin tana gida tare da su.
Bedroom ta koma tayi wanka daman tun kafin ta fara aikin tayi sallah, ta shirya cikin riga da siket na atamfa, sannan ta fito parlour don har tara tayi. Ta gaishe da Umma ta amsa cikin fara'a da tambayarta ya ta tashi ta amsa da lafiya ƙalau.
"Daga tashi kuma sai aiki?"
"Haba dai Umma to ai ba wani abu ba ne nayi, tuni na saba."
Tare su kayi breakfast, sannan suka dawo kan kujerun parlourn, ta kalli Abba ta ce, "Wai Abba

da yaushe kayi wannann gidan ni har yanzu mamaki nake na sha wuya a can tsohuwar unguwarmu kowa ya ce bai san inda ka koma ba." Umma ta amsa da
"To wa ya kawo ki nan?" Ta sanar musu gidan redion su Hamma Umar Ta je da yadda su kayi da shi.
Junansu suka kalla, kafin Abba ya ce.
"Bayan aurenki mun tsinci kan mu cikin baƙin ciki da takaici na irin abinda ki ka mana, ba mu ɗauka asiri da tsafi ba ne jikinki sai daga baya inda muka gano wani ƙulli ne aka miki, nan take muka duƙufa addu'a da neman miki tsari.
Hakan bai ɓata zumincin da ke tsakaninmu da ahlin Umar ba sai ma sabon zuminci da mu ka kulla, ashe suma asalinsu 'yan jahar katsina ne. Mahaifinsa su biyar ne gurin iyayensu maza huɗu mace daya, Alkasim Inuwa magaifin Umar shi ne babba a gidansu sauran ƙannansa ne, gidansu sunyi karatu mai zurfi hakan yasa yawancinsu duk ma'aikata ne, shi kuma babban ɗan kasuwa ne, Umar shine ɗa na uku gurin iyayensa sai dai biyun duk sun mutu shine kawai ya rayu hakan yasa iyayensa ke ƙaunarsa sosai duk da bayan shi sun sake biyu suma duk ba rai, sai dai sauran 'yan uwansa sun haifafa sosai suna da yawa. Zubaida ɗiyar ƙaramar ƙanwarsu Alhaji Alkasim ce ita ce 'ya ta huɗu gurin mahaifiyarta, tunda ta taso take ƙaunar Umar har takai da faɗawa kakaninsu tun suna da rai kakansu ya ce ko bayan ransa Umar ya auri Zubaida, duk da dai shi Umar ɗin ba wani sonta yake ba, haka suka taso har zuwa yanzu da take matarsa, wannan gida da ki ke gani Umar ne ya mallaka mini shi halak-malak har da komai da ke ciki sannan ya buɗe mini babban shago ya zuba mini kayan hatsi da su manja da man gyada tare da yara masu sayar mini duk kyauta sannan ya bawa Ummanki jari tana sayarda sarƙoƙi da 'yan kunnaye kuma sosai sana'ar ta amsheta.
Shuru Sakinaa tayi har sanda Abba ya kai aya, hawayen farin ciki ne ke zubo mata tabbas tayi babban rashi wato rasa jarumi nagartaccen miji irin Hamma Umar. "Gaskiya naji daɗi sosai Allah ya saka masa da alkhairi shima Allah ya ba shi mai yi masa." Suka amsa da amin.
Rayuwar gidansu tana mata daɗi sosai sai dai cikas guda da aka samu yadda Hamma Umar ko yazo gidansu bai kula ta nunawa ma yake bai san da ita ba, abin yana mata ciwo sosai, duk idan yazo zata yi masa magana na gaisuwa amma bai amsawa ko kuma ya amsa a ciki-ciki.
Kamar yauma yazo gidansu sanye yake cikin ƙananun kaya ya yi masifar kyau kamar a sace sa a gudu, zuba masa ido tayi lokacin da suke magana da Umma wani irin maganaɗisun ƙaunarsa ke fuzgarta, tabbas Hamma Umar ya kai duk yadda ake buƙata a wajen ɗa namiji, ta shagala sosai da kallonsa har bata san lokacin da Umma ta bar parlour ba, sai jin saukar ruwa tayi a fuskarta, a furgice ta dubesa, ruwan da yake sha ne ya watso mata, daure fuska ya yi sosai kamar wanda bai taɓa dariya ba ya ce, "Kallon na mene ne har haka? Ya isa haka abeg."
Sosai taji kunya ta sadda kanta ƙasa, a hankali ta ɗago ta sake dubansa, gani tayi har ya miƙe ya fita, da sauri tabi bayansa, yana ƙoƙarin shiga mota ta kira sunansa, "Hamma Umar!"
Tsayawa ya yi ba tare da ya juyo ba.
Ƙarasowa tayi hawaye ne ya wanke fuskarta.
"Don Allah Hamma Umar kayi haƙuri ka yafe mini wallahi na ga ne kuskurena Nayi nadama duk da ban san na aikata ba amma na yarda KUSKURENA NE sannan tabbas nayi gudun gara ne na faɗawa gidan zago. Nayi danasani Hamma Umar kai ne ka dace da rayuwar Sakinaa sannan kai ne a bangon littafin labarin Sakinaa ka yafe mini ka karɓe ni a karo na biyu.
Wani mugun kallo da ya aika mata ya saka ta daidaita natsuwarta, a hankali kuma tayi ƙasa da

kanta hawaye na zuba.
"Sakinaa ina so ki man ce da komai da ya taɓa faruwa a tsakanimu, ni tuni na man ce da komai kuma ba na tunanin yanzu zan iya tuna cewa wani abu ya taɓa faruwa a tsakanimu don haka kema kawai ki manta!" Yana ga ma faɗa ya shige motarsa tare da fuzgarta a gurin Sakinaa ta zube tana kukan takaici.
Ɓangaran su Hajiya kuwa. Mubarak ne da su Larah sai Zaliha zaune a cikin ɗakin da aka kwantar da ita dukansu cike suke da damuwa, ganin yadda lokaci guda Allah ya mayar musu da mahaifiya.
Larah ta goge hawayen da ke gangaro mata cike da tashin hankali ta ce, "Hajiya ako da yaushe ni mai faɗa miki gaskiya ce a kan abinda ki ke amma baki jin maganata, baki jin shawara yanzu ai ga irinta nan wa gari ya waya?"
Hawaye ne ke gangarowa fuskar Hajiya ba halin magana don bakinta ya karka ce, likitoci ma sun tabbatar da ta kamu da cutar nan ta rabin jiki, ko motsi ba ta iyayi sai dai akwantar a zaunar, kamar wani jariri. Amma zuciyarta duk da haka ba ta karye ba, cike take da taririn ɗaukar fansa, ba hawaye take da kuka ko da nasanin abin da ya faru da ita ba, hawaye take na yadda idan ta sami lafiya zata wulaƙanta rayuwar Zaliha, kai har Sakinaa bata jin zata bari domin ta san har da haɗin bakinta akan abin Zaliha ta ce.
Mubarak yaja tsaki tare da miƙewa ya ce, "No gaskiya Hajiya abin nan ya ishe ni bazan iya ba! Haba! Mu kenan kullum a cikin asibiti, nifa kin san ban jurar irin haka."
Hawaye ne ke ambali a fuskar Hajiya yaci gaba da cewa. "Wallahi kima dai na kuka don kukan ba damuna zai yi ba, abinda ke gabana ma ishe ni zan nemar muku tikiti ke da Larah a wuce dake India ko a dace." Kama hannun Zaliha ya yi su kayi waje wacce duk jikinta ya yi sanyi da wannan lamari.
Hajiya zuciyarta taci gaba da taririn ɗaukar fansa, tasan wannan abin ma da ya aikata Zaliha ce ta saka shi, tunda da ace bata asirce mata yaro ba ba zai faɗa haka akan ta ba yarda Mubarak ke matuƙar ƙaunarta, Larah ce ke ta rarrashinta duk tunaninta kukan nadama Hajiyar take....

_WATA MIYAR SAI A MAKOTA, MUJE ZUWA..._

*Albishir ga masu karanta Littafin WANKA DA GARI mutum 20 ɗin farko da suka fara biya to na musu rangwame akan su turo 400 kamar yadda na ce mutum 20 na farko don haka dama ce ga duk waɗanda zasu fara biya kafin book 1 ya kammala, da zarar na kammala book 1 duk mai buƙatar WANKA DA GARI zai biya kuɗi 700*

_Zaku iya turawa kai tsaye ta wannan account 0037219728 Fatima Rabiu Sunusi StanbicIBTC_
Shaidar biya ta wannan number 08104335144

Mutanenmu na ƙasar Niger zasu turo da 500f na katin Moov ko Orange ta wannan layin 08104335144 idan kuma na kammala book 1 zaku turo 700f ne, Na gode.

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUku
#LabarinSakina2024
_Gawurtattu uku 2024_

WANKA DA GARI...

©UmmuAffan.

*Book 1 Page 19-20*

Ina kuke mata? Mata nake magana waɗanda suka amsa sunansu na mata ba muna mata ba! Kaya ne masu inganci waɗanda zai mai rabo ke samu. Ki buɗe bakin aljihu Hajiyata kiyi gyara da ingantattun kayanmu na GHT muna da.
Royal jelly-karin Niima jiki yayi kyau yyi sulbi kamar tawarda.
Akwai Garlic oil _maganin infection sadidan ga tightening da yke ka sa skin kyau sa namiji sunbatu.
Muna da Ganoderma reishi _xai ciccciko Miki da gaba ya motso d shaawa ya matse mace gam Yana gigita maxa.
Sannan akwai Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Ba anan muka tsaya ba muna da irin su Constifree tea _masu kashi d tauri Yana sake ciki ya wanko duk wani dattin mara ya gyra skin yyi fresh.
Da su Longzit-matan da suka Kai shekaru 40 Niima y fara karanci a jikin su ku Sha longzit ku bn labari.
Ga Panicept_duk wani ciwon Kashi da gabobi in Sha Allah matsala t kau.
Kuma akwai Sto care_ina masu ulcer duk karfin ulcer in Sha Allah xai magance masu shekara da shekaru Basu Yi axumi b sun gwada sun fara axumi ynxu.
Da Female _masu matsalar alada , infection,rikecewar jini matsi duk wata harka t gaban mace in Sha Allah.
Duk abin da kake buƙata zaka samu daga GHT sayen nagari mai da kuɗi gida kai tsaye kayi wa wannan number mgn domin haɗaku da sha yanzu magani yanzu wato Maman Amal GHT 08104335144

Shahararru goma a duniyar kayan mata Maman Zee ƙamshi and Kayan mata, duk wasu nau'i na kayan mata na gargajiya da na zamani gumba tsumi tabaje zuma masu ƙyau da inganci ku nemi maman zee ƙamshi an kayan mata a number kamar haka 0806 384 5136 Tana Bauchi tana aika kayanta gari-gari Kasa-ƙasa. Sayen na gari mai da kuɗi gida.

*Masu buƙatar ɗaura musu tallah suyi mgn cikin farashi mai sauƙi.* A saman rubutu ko a ƙasa ko wanne da farashinsa. Na gode.

Wace ce Hajiya?

Hajiya Ruma mahaifinta ƙasurgumin boka ne wanda yake sana'ar bokanci da tsafi, ita ce 'ya ta biyar a gurinsa, yana mugun sonta saboda komai nasa ta biyo, wato ita ce tayo gadonsa. Tuntana ƙarama take zuwa ɗakin tsafinsa tana ganin yadda yake komai harta gajesa, bayan mutuwarsa taci gaba da komai, haka take ba arabi ba boko,
Mahaifin su Mubarak kuwa ta haɗu da shine sakamakon wasu abokan hamaiyarsa da suka kawo matashi akan tayi wani aiki da zai durƙufar da shi kasancewarsa ɗan siyasa, haka nan da tsafinta ya nuna mata photonsa taji duk duniya babu wanda take so sama da shi, inda ta masa wani surkulle da asirinta tasa mata sonta, haka suka yi aure, bayan zuwanta ta korar masa uwargida, matarsa ta fari kenan, daman ba su haihu da uwargidansa ba, shekara guda ta haifi Mubarak kuma tana sana'arta ta bokanci har zuwa lokacin. Sai dai shi Alhaji Sani mahaifinsu Mubarak bai san da maganar bokancin ba to min ta rufe komi ta riga ta asirce shi.
Bayan Mubarak tayi Muhsin da gashi sai Larah, ganin irin dukiyar da Alhaji Sani ya tara domin bayan siyasa yana kasuwanci hakan yasa ta masa abinda ya kashe shi har lahira, daga nan ta rufewa 'yan uwansa baki ko gidan ba su taɓa zuwa ba, haka tare ni yaranta ba arabi sai dai karatun boko sun yisa sosai kuwa har zuwa matakin Mesters. Duk a yaranta tafi son Mubarak su kan su ƙannansa sun san da haka tun suna jin haushi har suka  bari. Larah itace kawai ta biyo mahaifinsu a halaye sauran kuwa duk Hajiya su ka biyo.
Sannan tunda tayi aure bata ƙara waiwayar gida ba sai ƙaninta Saminu kawai da suke tare shima don yazo gidanta ne shine fa ta ba shi sana'a har ya yi aure shima ya tara iyali.
Hajiya tayi wata ajiyar zuciya bayan tuno wannan da tayi, rayuwa kenan yanzu ita ce ta koma haka, ita kawai tasan irin zafi da raɗaɗin da take ji, domin ba ƙaramin ciwo take ji ba, amma ta san na lokaci ne, tunda likitoci na kula da ita zata sami lafiya har tazo ta tagayyara rayuwarsu Sakinaa. Tabbas tayi sake ɗan zaki ya girma, amma ita kan ta tsoran tsafin ta take, sai sun san sun taɓo 'yar boka jikar boka kuma bokanya.
Wajensu Sakinaa kuwa, ta roƙi Abbanta yasa Umar ya samar mata Addimision ta fara karatunta, ita ma burinta ta zama 'yar jarida kamar Hamma Umar.
Cikin ikon Allah kuma Abba na mishi magana ya nemar mata abin ku ga manyan ƙasa. Tun da ta fara karatu take sosai ta man ce kowa da komai, tana girmama iyayenta tare da kyautata musu.
Bazaka taɓa kallon Sakinaa ka ce wai ita ce ke da yara biyu ba, jikinta ya murje ta ƙara kyawu da haske kyakkyawar yarinya matashiya, sai yanzu ne fa take 22y yanzu ne take tashen kyawun komai nata daidai yadda ake so, ta samu ƙawarta ta makaranta Salma, ita ma natsattsaya ce babu ruwanta kamar Sakinaan karatunsu kawai suka sa a gaba, ranar da tasanarwa Salma ta taɓa aure har da yaranta biyu  nan take Salma ta ƙaryata ta ta ce bata yarda ba, sosai suka yi musu ta ce,

"Amma Salma me yasa baki yarda nayi aure ba har da yara biyu?" Salma ta ce, "Duk fa wanda zaki faɗawa wannan maganar Sakinaa ba yarda zai yi ba, wa zai kalleki ya ce ke ɗin ce kika taɓa aure har da wasu yara dubeki fa? Ta ƙarashe tana nuna jikin Sakinaa.
Murmushi Sakinaa tayi sannan ta ba wa Salma duka tarihin rayuwarta, shuru Salma tayi har da hawaye ta ce, "Tabbas Sakinaa kin ga rayuwa wannan shi ne kuwa Kinyi Gdun gara kin faɗawa gidan zago, kuma kin fahimci Wanka da gari ba shi maganin yunwa sai anjiƙa an sha. Amma duk da haka kar ki yanke ƙauna zuciyata na ba ni tabbas Hamma Umar zai dawo gareki, tunda har yanzu yana rayuwarki ita kuma Zaliha kanta tayiwa, duk da zuciyata na wasi-wasi akanta ta wani fannin fa ba ta da laifi."
Numfashi taja ta ce,
"Ni yanzu ba na ta Zaliha wallahi taje da Mubarak ni babu wanda na tsana sama da shi, a yanzu burina Hamma Umar ya dawo gare ni." Ta ƙarashe da hawaye, share mata hawaye Salma tayi.
"Sakinaa ki kwantar da hankalinki ki sa a zuciyar tamkar ya dawo gareki, kar ki man ce yana cikin rayuwarki tsamo-tsamo balle idan ya kalli kyakkyawar surar nan taki uhmmm wallahi ke 'yar baiwa ce yaranki biyu amma jibarki har kin fini ni budurwa komai." Tare suka sa dariya.
"Ke ko baki da dama Salma."
Tana komawa gida tun a farfajiyar gidan taga motoci guda biyu, kallonsu tayi tare da ƙarasawa ciki a zuciyarta tana cewa 'baƙi mu kayi kenan gidan?'
Haka ta shiga ciki cikin sallama, su wa za ta gani? Daddyn Umar da wasu jama'a masu yawa, tana shugowa suka saka mata ido, da sauri ta ƙarasa tare da zubewa har ƙasa tana gaishe su suka amsa cike da fara'a da sakin fuska.
Ta yi wa su Umma sannu da gida sannan ta shige ciki tana mamakin me ya kawo dangin Umar gidansu, wanka ta shiga tare da ɗauro alwala ta zo ta gabatar da sallah.
Da dare suna zaune a parlour da su Ummanta, Abba ya ce,
"Sakinaa kin san me ya kawo Su Daddyn Umar?" Ji tayi gabanta ya buga da ƙarfi cikin dauriya ta ce, "A'a Abba." Gyara zama yayi sannan ya kalle ta.
"Sun zo neman auranki ne, tunda tuni ki ka gama iddarki kuma harkin fara karatu." Sosai take kallon Abba cike da mamaki da al'ajabi ta kasa ga ne yanayin da take ciki farin ciki ko akasin hakan? Abba ya ci gaba da ce wa,
"Sai dai wannan karon ban yi saurin yanke hukunci akan ki ba saboda ba na so ki sake ba ni kunya a karo na biyu na ce suje zan tuntuɓe ki idan kin amince zan kira su."
Hawaye suka fara zubo mata a fuska inda tayi ƙasa da kanta ba kukan komai take ba sai na abinda Abba ya ce ita nasan ko wancen karon ba don abinda aka mata ba babu abinda zai sa ta tsallake maganar Abbanta.
Umma ta ce, "Me na faɗa maka? Shiyasa na ce karka ce ka amince gara ka fara tuntuɓarta kafin ta sake zuba mana ƙasa a ido ka ga alama dai ko?" Da sauri ta zube ƙasa bi sa gwiwowinta ta ce, "Abba da Umma ku gafarce ni, ko waccen karon akasi aka samu amma don Allah kuyi haƙuri ku yafe mini ku dai na tuno baya, ni na amince da auren Hamma Umar wallahi ko a gobe za ku ɗaura mini aure da shi to a shirye nake kuma zan masa ladabi da biyayya daidai iyawata, bazan taɓa ba ku kunya ba iyayena."
Umma ce ta ɗagota ta rungume tana buga bayanta alamar rarrashi "To ya isa haka mu tuni muka ɗ yafe miki Sakinaa babu komai aran mu."
Abba ya ce, "Allah ya miki albarka Sakinaa tabbas tuntuni mun yafe miki don haka ki dai na

tuno komai aran ki." Share hawaye ta fara.
"Na gode Iyayena."
Washe gari suna zaune a kan kujerun roba cikin makarantarsu Sakinaa ke sanar da Salma abinda ya faru, ta ɗaura da cewa, "Salma abinda idan na tuno yake faɗar mini da gaba shi ne ina ji a jikina kamar ba da sanin Hamma Umar ba aka zo gidanmu neman aure na."
Salma ta ce, "Wannan ba lokacin wannan tunanin ba ne, domin ko da bai sani ba idan kin je gidan zai sani. Ke fa mace ce kin san duk hanyar da zaki dawo da hankalinsa gareki, sannan kuma yana son ki a baya har yanzuma ina kyautata zaton yana sonki don haka ki cire komai aran ki, mu fara shirin biki." Bugun wasa ta kai mata ta goce, "Ba wani shirin da zan yi yasin."
Salma ta ce, "Shiri fa ya zama dole, kin ga ƙanwar Mamana tana shiri na gyaran amare komai ya yi zom-zom zan haɗaki da ita kin san Shuwa ce ita tasan sirrin komai, ai Maman Amal ƙarshe ce da tasan sirri na gara masu inganci mai so na haɗa su ya yi magana ta wannan number 08104335144 ita ake kira mai da tsohuwa yarinya." Sakinaa ta ce, "Wallahi Salma ba ki da dama Allah ya shirya ki amma dole na ziyarci Maman Amal GHT domin dawo da martabata daga Hamma Umar."
"Amin amma fa dole ki gyara ko da baki da kishiya balle akwai." Sai lokacin gabanta ya buga da ta nuno ashe wai tana da kishiya. Zubaida ta tuno lokacin da ta ganta a gidan su Hamma Umar da ya taɓa kai ta, gabanta ya sake bugawa tuno abinda ya faru da irin kallon da take mata.
Sosai aka fara shirye-shiryen bikin Sakinaa da Umar. Inda shi ta ɓangaransa bai san komai ba kamar yadda Sakinaa ta hasaso, Daddynsa ne ya yi komai shi kuma dalilinsa nayin hakan, tun bayan da Sakinaa tayi aure har yanzu Umar ya kasa dawowa kamar da sannan ga babban rashin dacen aure da ya yi, duka familynsu sun san abinda ke faruwa a gidan Umar.
Zubaida dai muguwar ƙazama ce idan ka shiga bedroom ɗinta idan kai mai ƙanƙami ne sai kayi a mai saboda zan iya cewa tunda taje gidan bata taɓa shara ba da garan gado, da ta cire kaya duk inda ta samu nan take ajewa, abu dai babu kyawun gani Umar ya mata magana ta ce sai dai ya kawo mata 'yan aiki shi kuma ya ce bazai kawo ba, domin ko da cen shi ƙanƙami gare shi ko abincin 'yan aiki bai iyaci Mummynsa ke masa, amma ita kuwa bata girki ga shegen yawo yau tana gidan wancen ƙawa gobe ana bikin ƙawa, ko ƙanwar ƙawata ko ƙawata ta haihu, gashi ƙawayenta suzo su cika gidan su saka kiɗa su dun ga rawa ana ɗaurawa a Tiktok har da masu shaye-shaye ita kantan tana yi sai dai ba ta bari Umar ya gani.
Babu abinda ta sani sai wanka ta dinga tiƙa rawa tana ɗauka a waya ta ɗaura a Tiktok sai ka ce ba matar aure ba, sai kum fita unguwa idan a cikin gidan zaka isketa kuwa wata buguzun, tana zaune gida irin wannan tsaruwa ta ƙarshe ya yi amma idan ka shugo sai ka ɗauka 'yar aikin gidan ce, wanka sai za ayi rawa ko fita ta kecewa sa'a.
Ba ta san hakkin miji ba, yo shi Umar tun satin farkonsu da yasan ya neme ta bai sake bi takanta ba don shi mutum ne mai tsafta bazai iya da ƙazantarta ba, itan ma bata taɓa zuwa gurinsa da sunan wani abu ba kuma da bai nemanta ba ta ce masa mene ne dalili ba, haka suke rayuwa abin ba tsari tun Umar na dannewa har yazo ya fara mata magana akan ƙazanta da yawo amma taƙi shi kuma saboda zumincinsu ya rabu da ita sai dai ko kallo bata ishe sa ba, kusan kullum da azumi bakin sa domin kare kanka kuma a gidansu yake buɗa baki, wannan dalilin yasa iyayensa suka gane yana cikin damuwa da jarabawa, duba da irin son da yakewa Sakinaa yasa suka nemar masa aurenta sun san yana sonta wani dalilin nasa ne yasa yake ɓoyewa. (Cewar iyayen Hamma Umar ba ruwan Ummu Affan.)

Wata biyu kawai aka saka bikin, hakan yasa Umma ta fara ƙoƙarin gyaran 'yarta ciki da bai, Gurin 'yar mutan Bauchi wato shararru  goma a duniyar kayan mata, maman zeey ƙamshi da kayan mata, domin ita ma fa gyana ce fannin na gargajiya hakan yasa duk wasu kayan gyaran aure gurin Maman Zee Umma tayo oder domin gyara Sakinaa. Ɓangare guda kuma Ƙanwar Maman Salma wato Maman Amal GHT na nata aikin, hakan yasa kafin wata biyun ya cika idan ba sanin Sakinaa kayi ba ba zaka shaidata ba tayi kyau na musamman kamar ka saceta ka gudu. Duk mai son saya wani abu gurinsu ya tuntuɓe ni domin gyaransu iyaka ne.
Umar har zuwa lokacin bai san wainar da ake toyawa ba, bai san komai ba sai ana sauran kwana biyu ɗaurin auren, inda Daddy duk wani abu da ya dace ya masa shida abokin Umar ɗin Faisal suka tsara komai, a ranar da Daddy ya sanar masa a razane ya ɗago kai ya ce, "Daddy aure na kuma sauran kwana biyu, wace zan aura ni na faɗa muku zan ƙara aure ne?" Daddy ya ce, "Baka faɗa mana ba amma mu mun san kana cikin wani halin da ƙara auren naka ne mafita, kuma muna da tabbacin wannan karon zaka dace insha Allahu."
 Ƙasa ya yi da kai,
"To Daddy wai wace ce zan aura ne?"
"Sakinaa."
Da sauri ya kalli Daddy tare da zuba masa ido, bazaka taɓa gane yanayin da yake ciki ba.
Daddy ya ce, "Umar tun farko Sakinaa ka ke so kuma ita ce ta dace da rayuwarka ina da yaƙinin zaka sami farin ciki daga gareta, ka san rabo tun farko rabon yaran cen ne ya kai ta gidan wancen mijin, kasan wani baya haihuwar yaran wani, dole kuma sai da taje ta ba sa rabon dake tsakaninsu sannan ta dawo gareka."
Shuru ya yi yana jujjuya kalaman Daddynsa a kwanyarsa kafin ya ce, "Daddy ba komai Allah yasa hakan shi ne mafi alkhairi, amma da za a ɗaga bikin zuwa wani lokaci na ɗan yi tunani."
"Tunanin me Faruuƙ sai ka ce wani ƙaramin yaro, kai dai kawai ka sawa abin albarka."
Kasa cewa komi ya yi ganin haka Daddy ya ɗauko wani zancen suka ci gaba.
Ana gobe biki Zubaida ta sami labari, cikin masifa da bala'i ta nufi bedroom ɗin Umar tana zuwa ta banka ƙofar ta shiga, zaune yake yana aiki a computer. Tana zuwa ta wani ci burki gabansa tana cika da batsewa ta ce, "Algungumi yau asirinka ya tonu daman aure za ka yi baka sanar mini ba, wannan wanne irin rashin mutumci ne?"
Duk da maganarta ta ƙona masa rai amma ko ɗagowa bai yi ba bare ya kalleta asalima duƙufa ya yi aikan da yake, ita kuwa hakan da ya yi ya ƙara ƙona ranta nan ta fara girgiza ta ce, "Umar da kai fa nake magana amma kayi mini banza kamar ba ka jin me nake cewa, ko yau ka kurum ce ne?" Nan ma shuru ya mata, ture computer gabansa tayi da ƙarfi, ai kuwa sai gata a ƙasa.
Cikin wata irin zuciyar da bai san yana da ita ba ya miƙe tare da kwasa mata wani lafiyayyen mari har sau uku, ai nan take ta ruɗe ta fita a haiyacinta ta riƙe kuncin tana wani matsananincin kuka, tuni bakinta ya fashe ganin jini ta saki wata ƙara tana kururuwa, tare da nufarsa da niyyar cukukuyarshi, ai duka hannayenta ya haɗa waje guda ya wani girgiza su tare da sakinta nan take ta zube tana harfe hanyen don ko miƙuwa sun ƙi tana kuka sosai. Kallonta ya yi cike da takaici ya ce, "Zubaida ina so ki sani kina cin darajar iyayenmu ne kawai amma da yanzu na man ce da tarihinki a rayuwata, don na zuba miki ido sai raini kuma ya shiga tsakaninmu? To aure zanyi goben idan kin isa sai ki hana sakarya ƙazamar banza kawai."
Ya fice ya bar ta ɗakin kuka sosai take da haka takai kanta nata bedroom ɗin, ta ɗau mayafi sai gida. Tunda ta shiga mahaifinta ke mata wani banzan kallo ya ce,

"Ke Zubaida lafiya kuwa?" Zubewa tayi gabansa tana kuka ta ce, "Abba saboda rashin mutumci irin na Umar da nuna mini ba ni da daraja a gurinsa ace zai yi aure ko ya sanar mini sai a bakin duniya nake ji, sannan na masa magana ya lakaɗa mini dukan tsiya har da zagina wai albarkacinku nake ci." Ta saki wani kuka wanda ke alamta irin zafin da turirin da take ji a zuciyarta.
Mahaifinta ya kalleta cike da takaici ya ce, "Wallahi Zubaida ke dai kin yi asara, shashasha wawuyar banza kina zaton duk abinda kuke ciki ba mu sani ba ne? To mun san komi mun san zaman haƙurin da yaron nan Umar keyi da ke, ban san ina kika kwaso wannan mugun halin ba. To don zai ƙara aure sai ki da mu? Auren da shi kansa bai san da shi ba sai jiyan nan, to abinda baki sani ba da ni aka je nemar masa auran."
Da sauri ta kallesa tana kuka. Ya ce, "Eh kwarai da gaske don haka ki tattara ki koma gidan mijinki kamar yadda kika fito da ƙafarki kafin in saɓa miki, idan kin je kin gyara halinki kanki kika wa idan ma baki gyara ba duk kanki kika wa, kima gode Allah da Umar ya iya zama da ke."
Hannu Zubaidaa ta ɗaura aka ta tare da rushewa da wani gigitaccen kuka, daidai fitowar mahaifiyarta daga bedroom....

Ƙara-ƙaƙa-ƙaƙa, anan na kawo ƙarshen littafi na ɗaya wato book 1 domin karanta littafi na biyu sai ku biya kuɗin karatu 500 kachal mu antaya a book 2 Akwai tarin chakwakwiya a gaba.
Shin za a ɗaura auren Umar da Sakinaa? Zubaidaa zata koma gidan Umar? Idan ta koma wanne irin zama ne za suyi da Sakinaa? Ya zaman Sakinaa zai kasance da Hamma Umar shin har yanzu yana ƙaunarta ko kuwa? Ɓangaren Mubarak zai dawo gurin Sakinaa? Ya zamansu zai ci gaba da Zaliha? Shin Hajiya zata warke har ta ɗauki fansarta ko kuwa ƙaiƙayi ne zai koma kan masheƙiya? Ku biyoni a Book 2 domin amsa muku duka tambayoyinku. Wanda zai biya ga yadda tsarin yake a ƙasa..

*Albishir ga masu karanta Littafin WANKA DA GARI mutum 20 ɗin farko da suka fara biya to na musu rangwame akan su turo 400 kamar yadda na ce mutum 20 na farko don haka dama ce ga duk waɗanda zasu fara biya kafin book 1 ya kammala, da zarar na kammala book 1 duk mai buƙatar WANKA DA GARI zai biya kuɗi 700*

_Zaku iya turawa kai tsaye ta wannan account 0037219728 Fatima Rabiu Sunusi StanbicIBTC_
Shaidar biya ta wannan number 08104335144

Mutanenmu na ƙasar Niger zasu turo da 500f na katin Moov ko Orange ta wannan layin 08104335144 idan kuma na kammala book 1 zaku turo 700f ne, Na gode.

#WankaDaGari
#UmmuAffan
#GawurtattuUku
#LabarinSakina2024